Ebenezer International

AMPLIFYCHANGE

# KAYAN AIKI

## Na mai kula da Tsarin aikin HKLJH

### KUNDIN KOYASWA NA 3 :
### KAFA SADARWA DA ABUKAN AIKI
### DOMIN NEMAN AFUWA DA JAN HANKALIN MUTANE GAME DA AIKIN HKLJH

***«Duniya tana wahala ƙwarai, ba ta dalili miyagun mutane ba, amma ta dalilin shiru da mutanen kirki suka yi»***
Napoléon Bonaparte

Agusta 2019

# Abinda ke ciki


KALMOMIN FARKO 4

GABATAR DA KUNDIN ........ 6

0.1 Dalili ........ 7

0.2 Manufa ........ 7

0.3 Guri ........ 7

0.4 Hanyar tafiyar da aiki ........ 7

0.5 Abin da kundin ya ƙumsa ........ 7

SASHE NA1 : AIKIN HAƊIN GWIWA DA ABUKAN AIKI CIKIN FANNIN HKLJH ........ 9

1.1 Manufa da guri ........ 9

1.2 Ma'anoni : haɗin gwiwa da aikin haɗin gwiwa ........ 9

1.3 Aikin haɗin gwiwa daban daban ........ 10

1.4 Muhimmancin aikin haɗin gwiwa ........ 10

1.5 Riba da matsalolin da ake iya samu cikin aikin haɗin gwiwa ........ 11

1.6 Abubuwan da ke ƙarfafa aikin haɗin gwiwa mai inganci ........ 11

1.7 Jigajigan abutar aiki mai inganci ........ 12

1.8 Matakan abutar aiki da haɗin gwiwa ........ 13

1.9 Aikin haɗin gwiwa da abutar aiki : misali na PINCER ........ 15

SASHE NA 2 : NEMAN AFUWA DA JAN HANKALI MAI INGANCI CIKIN FANNIN HKLJH ........ 17

2.1 Neman afuwa da jan hankalin mutane ........ 18

2.2 Abubuwan da suka yi kusa da neman afuwa ........ 20

2.3 Guri daban daban na neman afuwa ........ 22

2.4 Matakan neman afuwa ........ 22

2.5 Hanyoyi uku na neman afuwa ........ 25

2.6.Ma'amala tsakanin neman afuwa, ƙungiyar fara hula, da cigaba ......... 26

2.7 Neman afuwa da siyasar aikin gwamnati ........................................ 28

2.8 Abubuwan farko kafin a fara neman afuwa.................................... 29

2.9 Farilai na farko na neman afuwa...................................................... 34

2.10 Dubaru da kayan aiki na neman afuwa........................................... 36

2.11 Matakai da kayan aiki na dubarar neman afuwa............................ 38

ABUBUWAN DA AKE IYA DUBAWA............................................................................................................ 53

## KALMOMIN FARKO

**Ofishin bada Shawara da tallafi ta fannin Tarbiyya daga Tushe da ake kira (CAEB)** ya san da muhimmancin neman afuwa da ƙarfafa iyawar Ƙungiyoyin Fara Hula game da al'amarin kare Hakin mutane, ta fannin Kiyon Lafiya da ya shafi Jima'i da Haifuwa (HKLJH).

An shimfiɗa dokoki da farilai da yawa na ƙasa da ƙasa domin a tabbatar da hakin ɗan Adam gaba ɗaya, da kuma HKLJH daga cikinsu:

- Jerin ayukan cigaba mai ɗorewa daga nan zuwa 2030 ;
- Kundin Majalisar Ɗumkin Duniya da aka sa hannu a kanshi a Francisco a shekara ta 1945
- Yarjejeniya ta ƙasa da ƙasa da ke kula da Hakin Yara Ƙanana da ake kira (CIDE) ta shekara 1990
- Kundi Hakin ɗan Adam da Al'umma na Afirika da aka shirya a shekara ta 1981
- Yarjejeniya ta Kundi Hakin ɗan Adam da Al'umma mai kula da hakin mata a Afirika, da ake kira « Yarjejeniyar Maputo » na shekara ta 2005.

Bunƙasa NDDH cikin masu aiki cikin fannin HKLJH, mataki ne mai muhimmanci na tabbatar da sa hannun marasa galihu cikin tafiyarda tsarin HKLJH. Yana sa a rabu da tunanin bada taimako shi kaɗai, ko biyan bukatu. Amma yana ba waɗanda aka ware damar su more ma hakinsu kamar kowa.

An shirya wannan kundin koyaswa, domin aiwatar da ayukan proje na Amplifychange da ya shafi ƙasashe 4 na Afirika ta kudancin Sahara (Burkina Faso, Guinée, Mali et Niger). Yana ɗaya daga cikin kundayen koyaswa 4 na «Kayan aikin mai kula da tafiyar da aikin HKLJH» wanda za ya ƙarfafa iyawar shugabannin ƙungiyoyi masu aikin neman afuwa, da suke cikin tsarin bunƙasa HKLJH cikin ƙasashen 4 da aka zaɓa a Afirika ta kudancin Sahara. A cikin kafa ƙungiyoyi masu kula da kare hakin mutane game da kiyon lafiya ta fuskar jima'i da haifuwa, wannan kundin koyaswa za ya ƙarfafa aikin haɗin gwiwa tsakanin ƙungiyar fara hula a cikin ƙasa, da wurare daban-daban. Wannan kundayen koyaswa suna cikin kayan aiki:

- Kundin koyaswa na 1: Yadda ƴan ƙasa ke ɗaukar niyya domin ƙarfafa amfanin da dokoki cikin aikin HKLJH
- Kundi koyaswa na 2: A gane, a kuma yi aiki da tsarin da aka yi bisa hakin mutane cikin fannin HKLJH
- Kundin koyaswa na 3: Shimfiɗa aikin haɗin gwiwa domin neman afuwa na samo ma mutane hakinsu, game da aikin HKLJH.
- Kundin koyaswa na 4: Kayan aikin na gwarzayen aikin waye ma mutane kai a kan aikin HKLJH, a cikin makarantu ko wasu wurare daban.

Abin da kundayen koyaswar suka ƙumsa, yana lura da yanayin siyasa, da zamantakewa, da tattalin arziki na ƙasashen, da yankunan ƙasashen, da kuma matsaloli da suka zama kangi ga aikin HKLJH, bisa ga bincike daban-daban da muka yi[1] da kuma abin da abukan aikinmu na cikin sauran ƙasashe suka ji kuma suka gani.

Kowane kundin koyaswa na kayan aiki, an shirya shi yadda za ya zama da sauƙin amfani da shi, inda akwai jagoran koyaswa na kundi cikin siffar PDF da Word, da PowerPoint na kundin, domin bukatun koyaswa nan gaba cikin ƘFH, da bidiyo da aka ɗauka tamkar misali mai kyau na masu koyar da ƘFH.

An shirya kayan aikin cikin harshe faransanci, aka kuma juya su cikin harsuna 4 (Bambaranci na Mali, Maninka na Guinée, Hausa na Niger et Mosanci na Burkina Faso) da kuma rubuntu makafi da ake kira Braille.

Muna fatan wannan kundayen koyaswa za su taimaka ma masu tafiyar da tsarin aiki na ƙungiyoyin da ke aikin bunƙasa HKLJH, su ƙware a cikin aikin kuzarantar da mutane, da sarrafa kuɗi da aka zuba domin kawasda ƙalubalan da suka shafi aikin HKLJH , tare da tabbatar da sa hannun marasa galihu cikin aikin.

---

[1] Les 11 études menées par Ebenezer International dans le cadre de la présente subvention stratégique sont les suivantes:

- Six (6) Analyse de l'Economie Politique du secteur DSSR respectivement au Burkina Faso, Mali, Niger, Guinée, Malawi, Zimbabwe, disponible en français. La version Anglaise est aussi disponible pour les études du Malawi et du Zimbabwe ;
- Analyse comparative ciblée de la littérature en lien avec les DSSR en Afrique de l'Ouest (Burkina Faso, Mali, Niger, Guinée), disponible en française ;
- Analyse comparative ciblée de la littérature en lien avec les DSSR en Afrique du Sud-Est (Malawi, Zimbabwe, Ouganda, Afrique du Sud), disponible en français et en anglais ;
- Sondage en ligne sur la satisfaction des citoyens sur les Droits à la santé sexuelle et reproductive pour les écoles secondaires et les universités avec 30 000 répondants dans 6 pays de l'Afrique subsaharienne (Mali, Burkina, Niger Guinée, Malawi, Zimbabwe) disponible en français ;
- Analyse de l'indice du pays favorable aux DSSR pour 6 pays de l'Afrique subsaharienne (Mali, Burkina, Niger Guinée, Malawi, Zimbabwe), disponible en français;
- Rapport sur la performance des droits à la Santé Sexuelle et Reproductive pour 6 pays de l'Afrique subsaharienne, disponible en français ;
- Formulaire d'évaluation de la performance des politiques DSSR, disponible en français.

## Yanayin da ake ciki

Ƙasashen Afirika ta Yamma da Yankin Kudanci Afirika, suna fuskatanr ƙalubalai da yawa: matsalolin yin aiki da dokoki, matsalolin fassara su, haɓakar ci da haikin mutane, matsalolin da suka zama kangi game da harakar magani, kasawar tabbatar da hakin mutane, rashin isassun kuɗi domin tafiyar da aikin kiyon lafiya, rashin daidaitattun farilai na aikin (HKLJH), bisa ga yadda ƙasashen duniya suka ɗauki alkawari.

AmplifyChange tana da gudummawa mai dubaru da ke da gurin :

- A nemi afuwa, kuma a taimaka wajen inganta siyasa da dubarar aikin HKLJH, dangance da abubuwa (darusa) na kan gaba na AmplifyChange cikin yankunan ƙasashe, cikin ƙasashe 4 na Afirika ta Yamma (Mali, Guinée, Niger, Burkina Faso) ;
- A sauƙaƙa ƙarfafa iyawar mutane game da kafa aikin haɗin gwiwa na ƙungiyoyin fara hula, domin iya aiwatar da aiki mafi kyau, bi sau-da-ƙafa na tasirin da siyasar aikin HKLJH cikin ƙasashen 4 na Afirika ta kudancin Sahara a Afirika ta Yamma (Mali, Guinée, Niger, Burkina Faso).

Banda wannan, projen yana aiki tare da ma'aikatu biyu cikin Afirika ta Yamma da Yankin Kudancin Afirika, wato:

- Ƙungiyar Kiyon Lafiya ta Afirika ta Yamma da ake kira (OOAS) a cikin Haɗin Kan Ƙasashen Afirika ta Yamma ta fannin Tattalin Arziki da ake kira (CEDEAO) a Bobo Dioulasso, a ƙasar Burkina Faso;
- Asusun Majalisar Ɗumkin Duniya mai Kula da Al'umma (UNFPA), mai cibiyarsa a Afirika ta Yamma a Dakar, ƙasar Sénégal.

Wannan gudummawa mai dubara ta AmplifyChange aikin haɗin gwiwa na ƙungiyoyi 4 (CAEB, Haɗin gwiwar ƘFH domin sake salon tafiyar da tsarin iyali a Afirika ta Yamma mai aikin da harshen faransanci, Ebenezer International et Humanité & Inclusion) domin tsawon shekara biyu ( 2 ) ,  daga  1 ga watan Nobamba na 2018 zuwa 31 ga watan Oktoba na 2020, inda **CAEB** ce ke shugabanci. Tana ba ƙungiyoyin da ke cikin wannan ƙawance damar su yi aikin neman afuwa, su kuma tafiyar da ayukan ƙarfafa iyawar ƙungiyoyi domin a inganta siyasar aiki da dubarun HKLJH, cikin ƙasashe 4 na Afrika ta kundanci Sahara a Afirika ta Yamma (Mali, Niger,  Guinée da Burkina Faso), tare da kan ziyara ta musanyar bayanai da kwatanta binciken da aka yi cikin ƙasashen  Yankin Kudancin Afirika (Malawi, Zimbabwe da Ouganda).

An aiwatar da projen cikin yankunan ƙasashe biyu na Afirika ta kundancin Sahara :

- Afirika ta Yamma: Guinée, Mali, Niger, Burkina Faso ;
- Yankin Kudancin Afirika : Malawi, Zimbabuwe, Ouganda.

### 0.1 Dalili

Ta wannan dalili ne aka shirya waɗannan kundayen koyaswa huɗu na «Kayan aiki na mai kula da tafiyar da tsarinHKLJH ». An zaɓi kundin koyaswa na 3, mai suna «Shimfiɗa aikin haɗin gwiwa da abukan aiki domin neman afuwa da jan hankalin mutane cikin aikin HKLJH», domin a koyas ko a ƙarfafa haɗin gwiwar ƙungiyoyi domin bunƙasa HKLJH, masamman ta wurin neman afuwa da ake yi wurin masu sa hanun cikin aikin.

### 0.2 Manufa

Kundin koyaswar yana nufin gabatar ma masu kula da tsarin na abukan aikinmu, ko minene aikin haɗin gwiwa ko ƙawancen aiki da abukan aiki, cikin ƙoƙarin da ake yi na neman afuwa game da aikin HKLJH. Yana ba su kayan aikin da za su sa a yi tsari tare, da aiwatar da aiki tare da neman afuwa a dukan matakai. Manufar ƙarshe ta kundin, ita ce tabbatar da neman afuwa domin aikin HKLJH, da ƙawancen abukan aiki, da hangen sake dubaru cikin ɗan lokaci, a Mali, Guinee, Burkina Faso da Niger.

### 0.3 Guri

Wannan kundin koyaswa yana ba masu kula da tafiyar da tsari da projen HKLJH damar su:

- Saba da kafa aikin haɗin gwiwa, ƙawancen aiki, da jan hankalin mutane, da duk wani abu mai nasaba da haka;
- Iya bambanta ƙawancen aiki daban daban da kuma muhimmancinsu;
- Su sansance da ribar da ake samu, matsaloli da matakan kafa ƙawancen aiki;
- Iya koyo da misalin PINCER cikin neman afuwa domin aikin HKLJH;
- Sani matsayin ƙungiyar fara hula cikin aikin neman afuwa;
- Iya shirya tsarin neman afuwa ingantace domin aikin HKLJH.

### 0.4 Hanyar tafiyar da aiki

An shirya wannan kundin koyaswa bisa ga tafarkin sa hannun kowa da kowa, daidai da wannan hanyar tafiyar da aiki, mai matakai huɗu :

- **Mataki na 1 :** zaɓen mashahurin da za ya ƙirƙiro kundin farko;
- **Mataki na 2 :** Neman littattafai da munsanyar bayanai tsakanin jigajigan masu akin cikin HKLJH;
- **Mataki na 3 :** Yin amfani da shawarwari da aka samu cikin binciken da aka tafiyar da shi ƙarƙashin Ebenezer International;
- **Mataki na 4 :** Yin amfani da ƙarin bayanai da aka samu cikin wallafawar ƙarshe ta kundin.

### 0.5 Abin da kundin ya ƙumsa

Banda gabatarwa, kundi koyaswar ya tsaru cikin sashe biyu kamar haka :

- **Sashe na 1 : Kafa aikin haɗin gwiwa da abukan aiki cikin fannin HKLJH**

Sashe na 1 yana zance a kan manufa da gurin kafa aikin haɗin gwiwa, da ƙawancen aiki,

kafin ya bada ma’ana da irin haɗin gwiwa da ake iya yi, da muhimmancinsu. Sashen yana zance a kan riba da matsaloli da ake iya fuskanta cikin kafa aikin haɗin gwiwa, da kuma abubuwan da ke ƙarfafa kafa aikin haɗin gwiwa mai inganci. A ƙarshe, yana gabatar da matakai na kafa ƙawancen aiki da misalin PINCER.

- **Sashe na 2 : Neman afuwa da jan hankalin mutane game da aikin HKLJH**

Sashe na 2 na gabatar da zancen neman afuwa da jan hankalin mutane, da manufufi, da matakan neman afuwar. Yana gabatar da nasabar da ke akwai tsakanin neman afuwa, da ƙungiyar fara hula da cigaba. Yana zancen neman afuwa ta fuskar siyasar aiki, da ka’idodinta na farko, da farilai na tushe, da dubaru, da matakai.

## SASHE NA1 : AIKIN HAƊIN GWIWA DA ABUKAN AIKI CIKIN FANNIN HKLJH

### 1.1 Manufa da guri

Manufar wannan sashe na farko, ita ce ya nuna ma masu kula da tsarin/projen HKLJH, irin dama da zarafi da aikin haɗin gwiwa yake badawa, da kuma yaya za su iya morar su cikin aikin da suke tafiyar da shi a wani wuri, cikin ƙasa gaba ɗaya, da cikin yankunan ƙasashe, da ma cikin duniya duka, game da aikin HKLJH.

Guri: A ƙarshen wannan sashe, masu kula da tafiyar da tsarin/projen HKLJH za su iya:

- Fassara ko minene aikin haɗin gwiwa, da abin da ba shi ba ne haɗin gwiwa;
- Sansance muhimmancin aikin haɗin gwiwa;
- Sanin wane iri haɗin gwiwa ne;
- Iya kafa aikin haɗin gwiwa da waɗansu ƙungiyoyi cikin fannin HKLJH;
- Iya raba hanyayoyin da suke kyautata aikin haɗin gwiwa mai inganci.

### 1.2 Ma'anoni : haɗin gwiwa da aikin haɗin gwiwa

ƘFH/Ƙungiyoyin wuuri na Al'umma, a cikin aiwatar da tsari/proje, suna iya gane cewa yana da wuya su yi aiki yadda ya kamata idan su kaɗai ne. Ta dalilin haka sai su kafa hulɗa tsakaninsu cikin wata ƙungiya da ake iya kira haɗin gwiwa.

> **<u>Haɗin gwiwa</u>** shi ne a duk lokacin da wani gungun mutane ko ƙungiyoyi, inda cikin yardarsu, suke musanyar bayanai, ko suke aiki tare, inda kuma suke tsara kansu domin su kiyaye iya yi wa kansu (ƴancin su yi abubuwa).

**Akwai wasu jigajigan abubuwa da suke fitowa daga cikin ma'anar haɗin gwiwa:**

- Ya kamata hulɗa ta zama bisa yarda tsakanin mambobin haɗin gwiwar, tsakaninsu da haɗin gwiwar kan kanshi;
- Ya kamata a yi ayuka tare irin na yi mani, in yi maka ("badawa da karɓa") (misali, musanyar bayanai, ko yin aiki tare) ;
- Ya kamata a kiyaye iya yi wa kan kowa, da ƴancinsa a cikin haɗin gwiwar;
- Ya kamata kowa ya amfana da ayukan da haɗin gwiwar ke yi (wato ya zamana kowa da kowa da abin ya shafa, ya amfana da aiki).

> **<u>Aikin haɗin gwiwa</u>** shi ne a duk lokacin da ake sa haɗin gwiwar ya tafiyar da ayuka. Shi ne a kafa sadarwa da juna, a kuma ƙarfafa musanyar bayanai tsakanin da juna («badawa da karɓa») kuma ya zamana hulɗa ce cikin yarda. Aikin haɗin gwiwa yana sa ƙungiyoyi su cimma gurin da ke kafa wasu haɗin gwiwa.

**Wannan allo yana taƙaitar da bambancin da ke akwai tsakanin haɗin gwiwa da aikin haɗin gwiwa**

| Haɗin gwiwa | Aikin haɗin gwiwa |
|---|---|
| • Kusantar juna tsakanin ƙungiyoyi domin bin ƙayyadaddun guri daban daban<br>• Yana sa haɗin gwiwar cikin halin da ke sauƙaƙawa da hangen ayukan da ake son yi idan za a yi aikin haɗin gwiwar.<br>• Haɗin gwiwar yana nan ne kawai | • Yana nuna matakai da ayukan da za su sa a cimma gurin haɗin gwiwa.<br>• Aikin haɗin gwiwa ya fi haɗin gwiwa kan kanshi, saboda yana sa a cimma gurin da aka bayyana.<br>• Ana iya kafa haɗin gwiwa ba tare da haɗin gwiwar ya aiki ba.<br>• Aikin haɗin gwiwa na iya faruwa tsakanin ƙungiyoyi ba tare da an kafa sassan haɗin gwiwar ba.<br>• Aikin haɗin gwiwa shi aiki yake yi. |

## 1.3 Aikin haɗin gwiwa daban daban

Daga cikinsu ana iya zana wasu kamar haka :

1. Aikin haɗin gwiwa na mambobi, inda akwai mambobin wani gungun mutane, misali manoma, makiyaya zuma, ƙungiyar gwabraye, ƙungiyar masu asusun bada bashi, ƙungiyar masu aikin bunƙasa HKLJH;
2. Aikin haɗin gwiwa na wasu wurare, misali makiyayan zuma na wata jaha, Ƙungiyoyi masu Zaman Kansu (ƘZK) / Ƙungiyoyin Wuri na Al'umma, manoma, ds ;
3. Aikin haɗin gwiwa wanda aka kafa domin bin guri iri ɗaya;
4. Aikin haɗin gwiwa bisa ga irin yadda ake tafiyar da aiki, misali irin wanda ba dole sai da aza farilai ba, na inda ana aikin ko'ina, ko wanda wuri guda ne ake aiki.

## 1.4 Muhimmancin aikin haɗin gwiwa

Aikin haɗin gwiwa yana da muhimmanci saboda waɗannan dalilai:

- Yana ba mutane da ƙungiyoyi dama su kafa hulɗa tsakaninsu (misali hulɗa ƘZK/Ƙungiyoyin wurin na Al'umma da suke da matsayi iri guda na cigaba da ƙwarewa) da kuma (misali hulɗa tsakanin ƘZK/Ƙungiyoyin Wuri na Al'umma masu matsayi da ya bambanta na cigaba da ƙwarewa) da mutane da suke tafiyar da ayuka iri ɗaya.
- Yana taimaka ma ƙungiyoyi su san abin da ke faruwa, sauyin yanayin siyasa, sabobin hanyoyin tafiyar da al'amura, ds.
- Yana sa a raba ƙwarewar da ake da ita, da tsinkaye (sani da ganewa) a kan abin da ya shafi cigaba.

- Yana sa a samo kayan aiki, a kuma yi aiki tare da wasu ƙungiyoyi domin abin da zai amfani mutane da ƙungiyoyin da abin ya shafa.

## 1.5 Riba da matsalolin da ake iya samu cikin aikin haɗin gwiwa

Aikin haɗin gwiwa yana ba ƙungiyoyin da suke aiki tare riba kamar haka:

- Yana sauƙaƙa musanyar bayanai, samun koyaswa da iyawa, sani, ƙwarewa, kayan aiki, ds., ta wurin tsara taruwanni, bada koyaswa, wallafa littattafai da tsarin tafiyar da aiki tare. Dukan wannan yana inganta aikin ƙungiyoyin ta wurin samun ingantaciyar iyawa.
- Yana rage maimaita abu guda sau biyu.
- Yana haɗa ƙungiyoyi masu matsayin ƙwarewa daban daban, da masu fusaha da iya sarrafa kuɗi daban daban.
- Yana sa ƙungiyoyi su gane da abubuwan da ke iri ɗaya da waɗanda suka sha bambam, game da ganewa da sansancewar irin yadda sakewa da cigaba suke faruwa, kuma yana bada damar a cike giɓin da ke akwai.
- Yana sa a yi aiki tare domin a sami tasirin da ake biɗa (neman afuwa, sakewar siyasar aiki).
- Yana iya haɗa masu zuba jari da bada fusahar aiki, da waɗanda suke bukatar kayan aiki da tallafi.
- Yana sa ƙungiyoyi su taimaka ma junansu, su ƙarfara junansu, su kuzarantar da junansu, kuma su san da iyawar kowa.

Ana samun matsaloli kamar haka:

- Rashin gane niyyar juna daga wajen abukan aiki
- Rashin isasshen bada kai, har da jin tsoron raba bayanai;
- Rashin kuɗi domin tafiyar da aikin haɗin gwiwa;
- Rashin yarda game da ayukan da wasu mambobin haɗin gwiwar ke yi;
- Nisa da juna (nisan wuri tsakanin masu aiki cikin haɗin gwiwa)
- Siyasar ƙasa da ba ta taimakawa;
- Matsalar sadarwa (wayar talho, fax, akwatin gidan waya, rashin kai ga amfani da yanar gizo, ko ba ta aiki ) ;
- Matsalar al'adu mai sa bango tsakanin mutane;
- Matsalolin tafiyar da aiki da shugabanci.

## 1.6 Abubuwan da ke ƙarfafa aikin haɗin gwiwa mai inganci

Abubuwan da ke kyautata aikin haɗin gwiwa mai inganci, su ne:

- Kayyade hange da guri (na kusa da ana nesa) na haɗin gwiwa;

- Tafiyar da ayuka na ainahi masu riba domin dukan mambobi;
- Mambobi masu kuzari da za su yi aiki, masu wajibin daidaita tafiyar aiki, da kula da aiki, da kuma kula da kayan aiki;
- Kowa ya gane matsayinsa da wajibinsa, da aikinsa, da kuma yadda gungun mutanen ke aiki ;
- Zama da tunanin aiki tare da wasu, yarda kowa domin a so, kuma a ji daɗin aiki tare .
- Hali, yarda da wasu, yin aiki cikin haske, sahihanci, ƙarfafawa, ginawa, ƙauna, hanƙuri, nagarta, kula da bukatun wasu, lura da amfanin juna, nuna yarda, kada a yi wa wani laifi, tausayi, gafara, zama a shirye a karɓi koyaswa daga waɗansu, tawali'u, halin hidimtawa, kamun kai, tabshin hali, wajibi, isa dogara, iya jure ma kowane yanayi, mai iya sake ra'ayi, mai hulɗa;
- Ganewar fasalin shugabanci;
- A guje tattara aiki a kan wasu mutane kaɗai, amma a ba kowa damar ya sa hannu cikin aiki;
- A kakkafa haɗin gwiwa na ma'aikatu;
- Rabawa, zama cikin ƙungiya, da yarda da wasu (sa hannu cikin dukan ayukan haɗin gwiwa) ;
- Abin da yake daidai – aikin haɗin gwiwa na bukatar tallafi da yardar mambobi;
- Taimakon juna, dogara da juna da hanyoyin sadarwa masu inganci;
- Shirin tafiyar da ayukan haɗin gwiwa;
- Bin sau-da-ƙafa mai zurfi a kan kari, na ayukan haɗin gwiwa;
- Sa hannun masu amfana cikin aikin haɗin gwiwa domin a tabbatar da mutane za su ɗauki aikin tamkar nasu ne;
- Ladabta ma juna, da yaba matsayin kowa, da gudummawar kowa;
- Mayar da bayanai, koyo lokaci zuwa lokaci na tabi'un ƙwarai cikin haɗin gwiwar;
- Mutum ya sadaƙar da kansa domin manufa ta haɗin kai ;
- Hanyar gyara rikita da kowa ya yarda da ita;
- Sarrafa kuɗi yadda ya kamata – mutunci, baiwa da ƙarin gudummawa.

## 1.7 Jigajigan abutar aiki mai inganci

### 1.7.1 Mai kuzarantaswa

Mai kuzarantar da mutane, shi ne ya hamzartar da mutane su tashi su yi aiki. Yana tattara mutane domin su nufin hange guda. Idan aka fara cimma hange, to aikinsa ya ƙare, sai ya janye. Sai mutane su ci gaba da bin hangen da kansu.

Mai kuzarantaswa yana ɗaukar lokaci domin sadarwa. Yana ba mutane cikakkiyar dama, ba ya tsayawa kan ƴan ƙananan bayanai. Babu bincike, babu bada ranakun yin wani abu, babu bada umurnin yin wani abu: babu katsalandam.

Mai kuzarantaswa yana ƙarfafa iyawar mutane, yana kuma yarda da su, cewa suna iya yin aikin yadda ya kamata.
Yana bada hanya, yana kuma ba mutane damar su yi iyakar ƙoƙarinsu. Yana da matsayin mai bida wasa, kuma yana da hanƙuri. Irin wannan yana bada damar a ƙirƙiro sabbin abubuwa.

### 1.7.2 Mai bidawa

Kowace abuta cikin aiki tana bukatar mai bidawa domin ya kai ga haɗa abukan aiki tare, kuma ya sa su riƙe hulɗarsu. Abutar aiki da gungun masu aiki, suna fuskantar matsalar zaɓi tsakanin muradin mambobin gungun domin haɗin kai cikin abin da suke son yi, da nasu muradin, da abin da suke jira na masamman. Ana bukatar mai bidawa da ba ya goyon bayan wani ɓangare, wanda yake ganin komi gaba ɗaya, domin a samu kowa ya yi sadarwa yadda ya kamata, kowa ya bada haɗin kai domin a nufa wajen da ya kamata.

Mai bidawa yana taimaka ma mutane su iya gani, kuma su yi tunani a kan abin da za ya faru, da abin ya kamata su yi domin su cimma gurinsu. Yana tuna masu da ƙudurinsu lokaci zuwa lokaci, da tamaninsu na ainahi, yana kuzarantar da su, yana kuma hamzarta su su cimma hangensu. Domin wannan ya tabbata, yana taimaka masu su gina, kuma su ƙarfafa kyakkyawar hulɗa, da haɗa kayan aikinsu tare, ta wurin yin aikin mai hidima daga ɓoye, da daidaita al'amura domin abuta cikin aiki ta cigaba. Wannan yana nufin saurare da yawa da bukatar a taimaka ma mambobi su saurari juna, su yi cikakkiyar sadarwa.

### 1.7.3 Gwarzaye

Gwarzaye su ne shugabannin ƙungiyoyin matasa, da na mata, ds. Gwarzo, shi ne wanda yake da marmarin wani hangen nesa, da kuma yake bada kai sosai wajen bunkasa shi, kuma yake kan waɗansu ga su shiga cikin hangen nesan. Gwarzo yana iya sa wani abu ya tabbata, kuma ya ci gaba saboda yana samun yardar masu ɗaukar ƙuduri, da goyon bayan mutanen da suke aikin.

### 1.7.4 Masu ɗaukar ƙuduri

Mutane ne masu matsayin iko a cikin al'umma, cikin wani fanni ko cikin ƙasa, waɗanda suke bada «yardarsu» ko «goyon bayansu» wanda in banda shi, wani aiki ko proje ba zai iya ci gaba ba.

### 1.7.5 Masu aiwatar da aiki

Mutane ne da suke aiki tare da gwarzo, domin hangen da ake da shi ya tabbata.

## 1.8 Matakan abutar aiki da haɗin gwiwa

**Abutar aiki da aikin haɗin gwiwa suna bin matakai da ake iya taƙaitawa kamar haka:**

**Mataki na 1 : Bincike**

A wannan mataki ana sansancewa da abukan aiki na gaske da kuma muradinsu, da hangensu, da niyyarsu ta haɗa kai domin a yi aiki tare.

**Mataki na  2 : Horaswa**

Ana kai ga matakin horaswa a lokacin da abukan aikin na gaske suka yarda da su haɗa kai a yi aiki tare. Ana ƙayyade ƙuduri, matsayin kowa, ana tattaunawa kuma a kan tsare-tsare. Ana shirya hange, da aiki, da dubara da gungun mutanen da za su ƙaddamar da aikin.

**Mataki na 3 : Aiwatarwa**

Matakin aiwatarwa shi ne lokacin da aka yi aiki gadan-gadan a wurin da aka zaɓa. Masu ƙaddamar da aikin sun fara aiktawa bisa ga dubarar da aka zaɓa, ana kuma samun sakamako.

**Mataki na 4 : Nina**

A wannan mataki, abutar aiki ta fara bada sakamako, hulɗa ta kafu sosai. An horasda shugabanni, kuma suna iya horasda waɗansu shugabanni.

**Mataki na 5 : Yawaita**

Ana cimma matakin yawaita a lokacin da haɗin gwiwar ya haddasa wani haɗin gwiwa a wasu wurare. Shugabanni suna tabbatar da shugabancinsu yadda ya kamata cikin ƙungiyoyinsu, da kuma haɗin gwiwar. Suna kuzarantas da wasu shugabanni, suna kuma horasda da su, domin a tabbatar da tsara da za ɗauki aikin shugabanci nan zuwa gaba cikin haɗin gwiwar.


## 1.9 Aikin haɗin gwiwa da abutar aiki : misali na PINCER

Misalin “Pincer” wani misali ne na faɗa a ji wanda ya cancanta, domin a iya faɗa a ji cikin siyasar aiki a cikin dukan ƙasashe. Ana iya amfani da shi cikin ƙasa ko ma cikin al’umma. Kafa ƙawance da haɗin gwiwa yana ƙarfafa ƙoƙarin neman afuwa, saboda yana faɗaɗa faɗa a ji na masu aiki cikin wani fanni, kamar irin na kiyon lafiya da ya shafi jima’i da haifuwa.

Wannan farilai biyu suna tsakiyar wannan misali:

- shiga, da sa hannu, da kuzarantarwar na KZK, ko wasu ƙungiyoyi da masu amfana.
- Faɗa a ji cikin siyasar aiki da jan hankali da masu ɗaukar ƙuduri suke yi, da aikin sadarwa da kafofin yaɗa labarai, da dukan mutane.

**Hoto na misalin PINCER**




**PINCER : hanya ce ta ƙasa da ƙasa ta neman afuwa mai inganci**

Kibiyoyi suna nuna wane waje ne ake siyasar, da kuma wajen su wa ne siyasar ta nufa.

Ƙawancen suna kafuwa a cikin ƙasashe, ko wurare, saboda nan yake daidai a kafa su. Ƙawance suna haɗuwa tsakaninsu cikin yankunan ƙasashe, cikin ƙasashe da ƙasashe, kamar Kungiyar Hadin kan Kasashen Afirika ta Yamma (CEDEAO), Hadin Kan Kasashen Afirika, ko cikin duniya gaba ɗaya. Wannan ƙawance suna tsaruwa dangance da bukatu na masamman.

Ƙungiyoyi iri su Amnesty International (masu kula da hakin ɗan Adam), Greenpeace (masu kula da muhalli) ko Asusun Duniya mai kula da halittu (dabbobi da itatuwa) misali ne na ƙawancen ƙasa da ƙasa da aka sani sosai. Amma akwai waɗansu da yawa da suke fuskantar wasu bukatu iri iri, kamar su kasuwanci, noma, ruwa da tsabta, kiyon lafiya, hakin yara ƙanana da mata.

Bisa ga ka'ida, ƴan ƙasa da ƙungiyoyi da suke cikin ƙasarsu, a cikin ƙasar kaɗai ne suke iya faɗa a ji ta fuskar demokarasiyya. A matakin ƙoli na ƙasa da ƙasa, wakilan gwamnatotin ƙasashe da suke sa baki cikin tattaunawa a matakai daban daban, su ne suke yanke magana dangance da siyasar aiki.

Ga ƴan ƙasa na Afirika wadda take mamba ce ta Haɗin Ƙan ƙsashen Afirika, yana yiyuwa ta faɗa a ji a wurin majalisar Haɗin Kan Ƙasashen Afirikia da wurin ma'aikatan HKƘA(UA). Amma kowace ƘZK, tana iya faɗa a ji wurin gwamnatotin ƙasashe.

Aikin ƘZK mai bada tallafi ta Turai, ta kudu, tana iya taimakawa domin inganta siyasar ƘZK abukan aikinta da suke cikin wasu ƙasashe daban. Banda matsayinta na mai tallafawa, ƘZK na iya bada shawarar a ƙarfafa iyawarsu cikin fannoni kamar haka:

- Sani, bincike da nazari abinda ke faruwa cikin ƙasashe, da matsayin masu sasantawa na ƙasashen Afirika.
- Cigaban ma'aikatu abukan aiki, da haɗin gwiwa cikin ƙasashe masu tasowa;
- Ƙarfafa iyawarsu  dangance da fusahar sasantawa;
- Sauƙaƙa sadarwa ta kai tsaye da masu ɗaukar ƙuduri na ƙasa da na Afirika;
- Zuba jari domin masu jan hankalin masu bada kulawa su sadu da masu ɗaukar ƙuduri na ƙasa da ƙasa;
- Shiryawa da nazarin na matsayi na haɗin kai dangance da sha'anin siyasa.

Cikin sadarwa da yin taron gangami, ƘZK na kudu suna iya tafiyar da ayuka kamar  haka:

- Tanada bayanai cikin yanar gizo ta haɗin kai;
- Jan hankalin kafofin yaɗa labarai a lokacin da ya kamata domin ƙarfafa jan hankalin;
- Shirya gangami na cikin ƙasa da kuma na ƙasa da ƙasa;
- Zuba jari domin yin taron gangami cikin ƙasashe masu tasowa.

Kawance ƙungiyoyin fara hula masu kawo sabon salo cikin tsarin iyali a Afirika ta Yamma mai amfani da harshen faransanci, shi ne babban haɗin gwiwa na ƙungiyar fara hula da yake ta fannin HKLJH cikin ƙasashe  9 da suke cikin abin da ake kira Ƙawancen Ouagadougou - Mali, Guinée, Burkina Faso, Niger, Sénégal, Benin, Togo, Mauritanie, Côte d'Ivoire. Wannan ƙawance yana aiki da waɗansu ƙawance na duniya kamar su Family Planning 2020 (FP 2020 www.familyplanning2020.org

**SASHE NA 2 : NEMAN AFUWA DA JAN HANKALI MAI INGANCI CIKIN FANNIN HKLJH**




**Ede, Pays Bas – Maris 2010**

## 2.1 Neman afuwa da jan hankalin mutane

### 2.1.1 Ma'anar neman afuwa

Neman afuwa dubara ce da ƙungiyoyi masu zaman kansu, da gungun mutane masu muradi ɗaya, kafofin yaɗa labarai, da masu fafatakar wani dalili, har ma da masu ɗaukar ƙuduri suke amfani da ita cikin duniya, domin su faɗa a ji cikin al'amarin siyasar aiki da kawo sakewa.

Akwai ma'anoni daban daban na neman afuwa, da kuma hanyoyi dayawa na neman afuwar.

Neman afuwa fusahohi da hanyoyi da ake bi domin a kawo wata sakewa tagari mai ɗorewa a cikin tsare-tsare: na tattalin arziki, zamantakewa, siyasa, al'adu, muhalli, ta wurin taɗi tare da maɗauka ƙuduri daban daban. ''A fita daga cikin halin da ba a so, a shiga cikin halin da ake so''.

Neman afuwa, yi magana ne, jan hankalin al'umma ne game da wata matsala mai muhimmanci, domin a maida hankalin maɗauka ƙuduri zuwa ga warware ta.

A ƙarshe, neman afuwa dubara ce da ake amfani da ita domin a faɗa a ji wurin maɗauka ƙuduri a lokacin da suke kafa dokoki, da farila, suke rarraba kayan aiki, da kuma ɗaukar ƙuduri daban daban da suka shafi rayuwar mutane.
A cikin wannan kundi, za a yi amfani da ma'anar da Taro bisa Ingancin ƘFH ya bada, cewa « shi ne ayuka ne da aka tsara domin a faɗa a ji a kan siyasar aiki da ayukan mahukunta, domin a kai ga samun sakewa tagari mai ɗorewa. A nema kuma ya zamana kowa na iya sa bakinsa cikin matakan ɗaukar ƙuduri (yawanci mutane), ya zamana ana amfani da siyasar kare matalauta da waɗanda aka ware su». [10]

Manyan tunani da ake amfani da su cikin neman afuwa su ne:

- Sake siyasa, ko ra'ayi, ko tsarin wata ma'aikata;
- A bada dalilai domin a bada shawara a kan wani tunani gaban wasu mutane;
- Yin magana, jan hankalin wata al'umma game da wata matsala mai muhimmanci, kuma a maida hankalin maɗauka ƙuduri wajen warware matsalar;
- Aiki tare da wasu mutane ko ƙungiyoyi domin kawo bambanci cikin wani al'amari;
- A faɗa a ji a kan ra'ayin masu ikon ɗaukar ƙuduri;
- A bayyana wata matsala, a bada hanyoyin warware ta, kuma a yi abin da zai sa a ɗauki mataki game da matsalar, da kuma warware ta.

**Abin da ba neman afuwa ba ne:**

- Aza ma maɗauki ƙuduri tambaya cikin taro;
- Roƙon a taimaka ma wani matalauci ko wanda aka lahanta ma;
- Faɗaɗa aikin ƘFH;
- Bada bayanai, Sadawar, Tarbiyya ;
- Sanar da gwamnati ko masu zuba jari game da ƘFH;
- Sanar da gwamnati ko masu zuba jari game da tsarin ƘFH;
- Waye kai/ƙara bayyana ma mutane tsarin da ake ga aiwatar da shi;
- Biɗa ko tattara kuɗi.

### 2.1.2 Ma'anar jan hankalin mutane

Wata hanya ce ko fusahar neman afuwa inda ake amfani da sadarwa da bada bayanai (tsakanin mutum biyu) ga mutane masu faɗa a ji, irin masu kafa dokoki, ƴan fadar shugaba, Babban Zuzu, Paraminista, Shugaban wata ma'aikata, ko ma Shugaban ƙasa karan kanshi, ds.

Ana kusantar su da nufin a shayo kansu game da tamani da muhimmancin wata siyasa, ko doka, da irin sakewar da ake bukata a kawo.

**Abin da ba shi ba ne jan hankalin mutane**

- Ladabi,
- Nuna fin goyon bayan wani ɓangare,
- Aza tambayoyi,
- Hira marar manufa,
- Bincike,
- Nazari da tattaunawa a kan wasu matsalolin zamantakewa,
- Hira a kan matsalolin tattalin arziki,
- Tambaya shawara ko ra'ayi, ko wani taimako ta fannin fusaha,
- Sadarwa irin ta nuna ni ne mai gaskiya

[10] Guide de plaidoyer pour la promotion d'un environnement propice pour la société civile dans des contextes spécifiques développé par le Forum sur l'efficacité du développement des OSC pp.22

**Kwatanci tsakanin neman afuwa da jan hankalin mutane**

Neman afuwa da jan hankalin mutane suna da makamantan abubuwa da kuma waɗanda suka bambanta su.

| Abubuwan da ke cikin jan hankalin mutane | Abubuwan da ke cikin neman afuwa |
|---|---|
| • Ana yin abubuwa ba tare da an bi tsararrun matakai ba;<br>• Zance irin wanda ke nuna bukatar ɓangaren biyu su yi aiki tare domin kawo sakewar da za ta biya masu muradinsu;<br>• Sasantawa cikin ruwan sanyi, mai sassauci, mai manufa;<br>• Aiki tare kai tsaye, ko ba kai tsaye ba: ka samu-in-samu, a siyasance. | • Ana bin tsararrun matakai, ga sanin kowa ;<br>• Zance irin na ƙwato ma wani sashen al'umma ƴancinsa;<br>• Akwai siyasa da ɗaukar matsayi, da tsattsauran ra'ayi;<br>• Kariya/ɗauka matsayi da matsawa. |
| **Abubuwan da ke iri ɗaya** | |
| • Ayuka cikin tsarin tsari;<br>• Waɗanda aka nufa : maɗauka ƙuduri, ma'ikanta ;<br>• Masu amfana: waɗanda aka ware su (marasa ƙarfi, amma suna da nasu matsayi ta fannin tattalin arziki) ;<br>• Ɗauka matsayi, salon muhawara | |

## 2.2 Abubuwan da suka yi kusa da neman afuwa

Yawancin waɗanda ke cikin wannan aiki, har da ƙungiyoyin fara hula, suna gauraya kalmar neman afuwa da waɗansu. Wannan yana sa a yi kuskure cikin tafiyar da ayukan neman afuwa, inda a ƙarshe ake ganin kamar waye ma mutane kai ne da bada wata kulawa. Wasu suna amfani da wannan kalma tamkar wata hanya ko mataki na aiwatar da ayuka. Sun bambanta dagangace da masu tafiyar da aikin, mutanen da aka nufa, gurin da ake da shi, dubarun da ake amfani da su, da ma'aunin sakamakko.

| Kalmomi | Ƙungiyoyi | Mutanen da aka nufa | Gurin da aka nufa | Dubaru | Ma'aunin sakamako |
|---|---|---|---|---|---|
| **Bayani, Tarbiyya, Sadarwa (BTS) da sadarwa mai kawo sake halaye (SSH)** | Masu bada kulawa | • Kowane mutum<br>• Sashen al'umma (mata, maza, matasa) | A waye ma mutane kai, a sa su sake halayensu | • A tsara su dangance da mutanen da aka nufa,<br>• Watsa labarai<br>• Sadarwa zuwa ga al'umma<br>• Kafofin yaɗa labarai na gargajiya | • Sani da iyawa da aka samu da sake halaye tamkar alamun tafiyar da aikin,<br>• Taɗi mai maida hankali ga sha'anin lissafin adadi game da kulawar da ake badawa |
| **Hulɗa** | Masana'antu | Masaya | Inganta matsayin masana'anta, a kuma ƙara samun kasuwa | • Babbar tallatawa (radiyo, Tele, jaridu na rubuce)<br>• Taruwanni | • Inganta darajanta sunan masana'anta cikin mutane<br>• Ƙara samun kasuwa<br>• Inganta cinikayya |
| **Kuzarantar da al'umma** | Mambobi da ƙungiyoyi na al'umma | Mambobi da shugabannin al'umma | Ƙarfafa iyawar mutane domin su iya ƙayyade abubuwan kan gaba masu muhimmanci, kuma su ɗauki mataki | • Ziyara gida-gida<br>• Taron shawara na gari<br>• Hanyoyin Bincike da Tsara aiki tare da kowa (MARPP) | • Alamun tafiyar aiki da sakamako dangance da darasin da ake zance a kai<br>• Ingancin iri yadda mutane suke sa hannu cikin aiki |
| **Neman afuwa** | • ƘFH<br>• Ma'aikatun bincke<br>• Jami'o'i | Ma'aikatu na ƙasa da maɗauka ƙuduri | Sake siyasar aiki, tsare-tsare da inda ake sa kayan aiki | • A maida hankali ga maɗauka ƙuduri masu iya faɗa a ji<br>• Gurin neman afuwa<br>• A tsara taro tare da maɗauka ƙuduri<br>• A tsara taɗi tare da kowa (muhawara, taruwanni) | • Alamun tafiyar da aiki<br>• Aunawa da nazarin da kafofin yaɗa labarai suke yi<br>• Tambayoyi da da ake aza ma masu bada bayanai<br>• Gungun mutane masu taɗi a kan abubuwan da aka nufa<br>• Bincikien ra'ayin mutane<br>• Kundi siyasar aiki da aka amince da shi, dokoki da farilai |

An a yi koyi da : Le Plaidoyer/Lobbying. Hanya ta sa faɗa a ji da aikatawa a wurin maɗauka ƙuduri
*Disamba, wanda SNV ta wallafa, 2009*

## 2.3 Guri daban daban na neman afuwa

Neman afuwa yana samun tushe bisa ga wata matsala ta fuskar siyasa, kuma yana da manyan guri iri uku :

| Matsala | Gurin neman afuwa |
|---|---|
| Rashin siyasar aiki, da dokoki, da farilai | 1. Shimfiɗa siyasar aiki, doka, da farilai, |
| Rashin ingancin siyasar aiki, da dokoki da farilan da ke akwai | 2. A sake duba wata siyasar aiki, doka, da ke akwai |
| Rashin aiwatarwa yadda ya kamata, na wata siyasa, doka ko farilai | 3. Tabbatar da aiwatar da siyasar aiki, doka, da farilai yadda ya kamata |

## 2.4 Matakan neman afuwa

Ya kamata ƘFH, gungun mutane masu muradi iri ɗaya, su tuna da cewa idan aka ɗauki ƙuduri a wani mataki, yana shafar mutane a wani mataki daban. Kenan, idan ana son neman afuwa ya yi kyau, ya kawo sakewar da ake so, to sai in a yi shi a matakai daban daban. Wannan matakan sun bambanta dangance da mutanen da abin ya shafa, irin matsalar da ake fuskanta, mutanen da aka nufa, ko mai ɗaukar ƙuduri wanda ke da magana ta ƙarshe game da warware matsalar.

| Mataki | | Abin da ake hange | Waɗanda aka nufa/<br>Mai ɗaukar ƙuduri |
|---|---|---|---|
| **1. Cikin iyali** | | • Sake halaye da iyawar maza/mata, da iyaye | Maza, mata |
| **2. Wuri ko al'umma** | Cikin gari | • A inganta al'adu, sa mutane ga hanya, ƙuduri da wasu abubuwan gargajiya,... | Maigari, komitin garuruwa |
| | Cikin gungun mutane | • A iya faɗa a ji wajen zaɓen abubuwan kan gaba masu muhimmanci<br>• A iya faɗa a ji cikin aiwatar da siyasar aiki yadda ya kamata, da dokoki, da sauran ƙuduri da za a iya ɗauka<br>• Sake siyasar aiki, dokoki, da tsare-tsaren da ba a aikata su da kyau ba | Gungun mutane, Magatakardan gungun |
| | Cikin wani yanki | • A iya a faɗa a ji wajen zaɓen abubuwan kan gaba masu muhimmanci<br>• A iya faɗa a ji cikin aiwatar da siyasar aiki yadda ya kamata, da dokoki, da sauran ƙuduri da aki iya ɗauka<br>• Sake siyasara aiki, dokoki, da tsare-tsaren da ba a aikata su da kyau ba | Komitin yanki, Magatakardan yankin |
| | Cikin gunduma | • A iya a faɗa a ji wajen zaɓen abubuwan kan gaba masu muhimmanci<br>• A iya faɗa a ji cikin aiwatar da siyasar aiki yadda ya kamata, da dokoki, da sauran ƙuduri da aki iya ɗauka<br>• Sake siyasara aiki, dokoki, da tsare-tsaren da ba a aikata su da kyau ba | Komitin gunduma, Magajin garin Gunduma |
| **• Cikin ƙasa** | | • A iya faɗa a ji wajen shimfiɗa siyasar aiki, dokoki, da bada kayan aiki ;<br>• Sake dokoki, da farilai, ayoyin doka, siyasar aiki ta wasu fannoni, tsare-tsare, dubarun cigaba, ƙuduri, kundaye masu bayyana inda aka sa gaba, | Majalissa, Gwamnati, Ministoti, ma'aikatun gwamnati da makamantansu, Ƴan Sanda, Sozawa, Mashari'antu |

| Mataki | Abin da ake hange | Waɗanda aka nufa/ Mai ɗaukar ƙuduri |
|---|---|---|
| | wasiƙu, da bada kayan aiki... | |
| • **Cikin yankunan ƙasashe** | • A karɓa/a sake kundaye, furci, yarjejeniya, tsarin aiwatar da aiki, yarjejniya daban daban da aka yi cikin yakunan ƙasashe,.... | Ƙungiyoyi na cikin yankunan ƙasashe,(Union Africaine, ICCGL, TPIR, EALA, COMESA, EAC, CPGL,…) |
| • **Cikin ƙasashe** | • A karɓa/a sake kundaye, furci, yarjejeniya, tsarin aiwatar da aiki, yarjejniya daban daban da aka yi na ƙasa da ƙasa,....,.... | Ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa, ma'aikatun Majalissar Ɗumkin Duniya, Bankin Duniya, Asusun bada Lamuni na Duniya |

*Tableau adapté à partir de l'ACCORD, Boite à outils de plaidoyer pour les paysans d'Afrique, 2012 :27*

## 2.5 Hanyoyi uku na neman afuwa

Akwai hanyoyi uku na neman afuwa wanda sun danganta da yanayin da ake ciki:

- **Hanyar da ba ta dace ba**

Ita ce a duk lokacin da aka ƙi yarda da shawarar da mahukunta ko waɗanda abin ya abin ya shafa suka bada, ba tare da an bada wasu shawarwari ba.

- **Hanyar ta maida matani**

Hanya ce inda ake ƙin bada shawarwari, ko a ƙi yin komi; amma sai a jira har lokacin da wasu (gwamnati, jam'iyyun siyasa, wasu masu ɗaukar ƙuduri) suka bada tasu shawara, sai a maida matani.

- **Hanya aikatwa**

Hanya ce inda ake gano da matsalar da ake fuskanta cikin wani fanni da ƘFH take fata/wajibinta ne (a matsayinta na ƙungiya) ta yi wani abu, ta yi nazari, ta kuma samo yadda za warware ta, kanan ta bada shawara ga waɗanda abin ya shafa, masamman ƴan siyasa maɗauka ƙuduri. Wannan hanya ta ƙarshe, ta zama matakin da ke kai ga shirya dubara ta neman afuwa. Ta fi inganci, saboda ta fi bada yarda game da aiwatar da taron gangami na neman afuwa. Ita ce aka fi bada shawarar ƘFH su yi aiki da ita cikin aiki HKLJH.

## 2.6 Ma'amala tsakanin neman afuwa, ƙungiyar fara hula, da cigaba

- **Neman afuwa da Ƙungiyar fara hula**

Yawancin lokaci, ƙungiyar fara hula tana ƙumshe da fannoni, da mutane, da ma'aikatu waɗanda suke da matakai, ƴancin yi wa kansu, da ƙarfi da suka bambanta. Ƙungiyoyin fara hula suna cike da ƙungiyoyi irin masu agaji, masu zaman kansu da suke aikin cigaban ƙasa, ƙungiyoyi cikin al'umma, ƙungiyoyin mata, ƙungiyoyin masana'antu masu nasaba da addini, ƙungiyoyin ma'aikata, ƙungiyoyi masu taimaka ma kansu da kansu, ƙungiyoyi masu sha'anin zamantakewa, ƙungiyoyin masana'antu, da haɗin kan mutane masu matsawa domin a ɗauki matakai. A ganin ƙungiyar da ake kira World Alliance for Citizen Participation CIVICUS, ƙungiyar fara hula, wata dama ce inda mutane suka ƙirƙiro yanayi da ayuka, ƙungiyoyi da ma'aikatu domin su cimma biyan muradinsu tare.[11].

*Ƙare hakin ƙasa, ba goyon bayan waɗanda ke son su ƙare ikonsu ba ne. Ƙungiyar fara hula tana ɗauke da kyakkyawar akida mai amfani domin ƙasa: Yanayin kiyaye hakin ɗan Adam, adalci cikin zamantakewa, kiyaye hakin ɗan Adam, sarrafa ƙaddarar mutane cikin haske, samun kai ga haki na tattalin arziki da zamantakewa. Ta haka, tana ɗauke da kishin ƙasa na gaske.*

Ta dalilin haka, an san da cewa aikin ƙungiyar fara hula cikin shugabancin wurare daban daban ya ƙumshi abubuwa huɗu[12] :

1. Aikin *lauya* domin wakilcin muradin wuraren da take.
2. Aikin *kulawa* a cikin wurare ta fuskar tarbiyya, lafiya, tsabta, da noma, ds.
3. *Abokin aikin* gwamnati cikin tsarin cigaban ƙasa, tanadin kayan aiki, da ƙara gane yadda tsarin shugabanci yake tafiya.
4. Aikin *lura* da yadda gwamnati yake tafiyar da al'amuransa.

---

[11] World Alliance for Civic Participation. Civil Society Index 2010, pp.17
[12] AfriMAP, Une evaluation du role de la société civile dans la gouvernance au Mali 2007, pp1.

A cikin tsarin demokarasiyya, ƙungiyar fara hula tana da matsayi mai muhimmanci, a matsayinta na **lauya da mai tsaro da lura** (aiki na 1 da na 4) da irin yadda mahukunta da zaɓaɓɓun shugabanni suke tafiyar da aikinsu. Wannan aikin tsaro da lura yana farawa da lura da siyasar aikin gwamnati, lura da tafiyar da zaɓe. Amma aiki ya faɗaɗa zuwa ga bincken siyasar ƙasa, da yadda ake ƙayyade abubuwan kan gaba masu muhimmanci, aiwatar da aiki, yin adalci, da yadda ake raba kasafin kuɗi, da inganci kulawa da ake yi wa mutane.

Idan son samu ne, tsarin demokarasiyya mai cikakken iko, shi ne tsarin shugabanci da ke ba ƙungiyar fara hula matsayi mai muhimmanci **na bincike, da lura, da suka ra'ayi, da bada shawara ga gwamnati, game da sassan al'umma daban daban.** Shi ne neman afuwa na gaske. Matsayi ne wanda ya kamata a ce dukan sassan al'umma sun sami kansu a ciki. Amma, an gano da cewa can baya, ƙungiyar fara hula ba ta gane cewa wannan aikin nata ba ne, balle ma ta yi ƙoƙarin cika shi. Lalle ba dukan ma'aikatan ƙungiyar fara hula ba ne ke suke cika wannan aiki a kowane lokaci. Haka kuma ba kullum ba ne ake gane aikin fara hula a sarari ba. Amma ma'amalar da ke tsakanin ƙungiyar fara hula da aikinta na neman afuwa ana ganin ta a sarari, kuma ana fatan ta.

**Abubuwan da ya kamata a sani game da ƙugiyar fara hula**

Ƙungiyar fara hula:

- Tana aikinta cikin al'umma;
- Tana tsakanin gwamnati da hada-hadar kasuwa, da iyali;
- Ba ta nufin gungun mutane ko wasu ƴan ƙasa da suke rarrabe da juna;
- Tana nufin taron ƴan ƙasa da suke bin muradinsu;
- Tana hangen musanya tsakanin mutane da ke cikin cimma gurin daban daban na tare.

Ƙungiyoyi fara hula:

- Sun ƙumshi mutanen da suke da akida iri guda;
- Sun bambanta da gwamnati da kuma ƙungiyoyin da ke fafatakar tattalin arziki;
- Ba su aikin neman riba;
- Suna jan hankalin mutane a kan muradinsu;
- Suna aiki bisa ga niyyar da mutane suke da game da gurinsu, game da "ƙaddarar mutane"
- Ba su bin tafarkin aikin gwamnati, ko ɗaukar iko. Amma suna maida hankali ga sa hannun cikin siyasar aiki mai ƴancin kanta da demokarasiyya.

## 2.7 Neman afuwa da siyasar aikin gwamnati

- **Neman afuwa da siyasar aikin gwamnati**

Neman afuwa, hanya ce ta a faɗa a ji zuwa ga waɗanda aka nufa domin a sake siyasar aiki da irin yadda gwamnati ke tafiyar da aikinsa. Mataki ne mai tamani ga ƙungiyar fara hula. Hanya ce mai neman kawo sakewa cikin shugabanci, tabi'u, iko, hulɗa cikin zamantakewa, da matsayin ma'aikatu. [13].

Shi ne mataki na farko na aikin da ake son yi tare, inda ake tabbatar da cewa maɗauka ƙudurin siyasa na gwamnati sun san ra'ayin mutane, tun daga gundumomi har zuwa shugabannin ƙasa, ta wurin ƙungiyar fara hula. Babban muhimmancinsa, shi ne ya tabbatar da cewa siyasar aiki ta fiddo irin rashin adalcin da ake yi wa mutane, da bambancin da ke akwai tsakanin sassan al'umma; kuma ya zamana ana kiyaye hakin kowa, ana yi masa adalci, akwai yanayi mai kyautata ma kowa, a yardar ma kowane ɗan ƙasa ya sami dama da sa'a kamar kowa.

Idan ana son neman afuwa mai inganci, to dole sai an maida hankali ga abin da ya kamata a sake, a kuma gane yadda siyasar aiki take tafiya, da kuma yadda sakewa za ta faru.

- **Neman afuwa da cigaba**

A cikin yanayin cigaban tattalin arziki da na zamantakewa, neman afuwa yana hangen sake siyasar iaki, da dokoki, da farilai, rabon kayan aiki, da bin sau-da-ƙafa na aiwatar da ƙuduri daban daban da aka ɗauka, da suka shafi rayuwar ƴan ƙasa. Yana magana ne da maɗauka ƙuduri, masamman ƴan siyasa, masu kafa doka, manyan ma'aikata, da kuma shugabannin sassa masu zaman kansu, da aikin cigaba waɗanda ƙudurinsu na iya shafar cigaba da halin rayuwa da ƴan ƙasa suke ciki. Neman afuwa domin matalauta, yana cikin aikin cigaba na ɗungum, inda yana nufin kafuwa bisa ga ƙuduri daban daban na siyasa, da tsaro da lura na muradin matalauta, da marasa galihu, da rashin adalci, da wariya, ko mutane masu fama da nakkasa. Kenan neman afuwa shi ma siyasa ce, ingancinsa kuma ya danganta da ganewar da ake da ita game da siyasa, domin yi nazarin a kan illarta da tasirinta, bisa ga halin tattalin arziki da zamantakewar mutane.

Ma'amala tsakanin neman afuwa da cigaba tana nuna waɗansu fusahohi da aka fi amfani da su; daga nazari dalilan matsaloli zuwa niyyar da ake ɗauka na bin sau-da-ƙafa na siyasa, taɗi, sasantawa, da'awar ƙwato haki, sabbin proje da zu su sa a sanar da shugabanni, a kuma faɗa a ji cikin siyasar aiki mai zuwa, tsare-tsare da projen cigaba domin matalauta.

[13] Water Integrity Network (2009). Guide de Plaidoyer. Boîte à outils pour des actions en faveur de l'Intégrité de l'Eau, p.8.

## 2.8 Abubuwan farko kafin a fara neman afuwa

Ingantacen neman afuwa bisa ga siyasar aikin gwamnati ba ya da takala da za a ce a yi amfani da ita ko'ina. Dole a yi cikin tsarin tsari, a tsara lokaci, a yi shi cikin ɗa'a, a kuma yi yadda kamata. Saboda haka, nazarin abubuwan farko, masamman yanayin da ake ciki, sani, goyon bayan farilai masu muhimmanci na neman afuwa, sun zama dole, kuma ya kamata kowace ƙungiyar fara hula ta kiyaye su.

- **Nazarin yanayin da ake ciki**[14]

Yana da muhimmanci, ya zamana ƙungiyar fara hula da take so ta shiga cikin aikin neman afuwa ta fara da auna kanta, ta yi nazarin yanayin da take son tafiyar da aikinta; kafin ta shimfiɗa dubara, ta kuma fara aikin na neman afuwa. Cikakkiyar ganewa game da abubuwan da ke waje da na cikin gida, da suke iya sa a ci nasara ko a kasa, tana sa a san irin hanyar da za a bi, da irin ayukan da za a yi, da za su kawo tasiri mafi muhimmanci. Wannan yan tunas da nazari a kan abin da ake kira SWOT (Ƙarfi, kasawa, zarafi, barazana) da aka ganin cikin sashe na farko.

Kamar yadda aka gani, wannan kayan aiki na nazari, ya shafi sakankancewa da nazarin Ƙarfi, da Kasawa, da Zarafi, da Barazna (ƘKZB).

Yana sa mu yi tunani a kan ƙungiyarmu (daga ciki) da yanayin da muke ciki (daga waje), kuma ya zama mataki na farko da za ya taimaka mana mu ƙarfafa iyawarmu, mu kuma iya guje ma tarko lokacin aiwatar da dubararmu ta neman afuwa. Nazarin ƘKZB na sa mu yi tunani a kan yadda za mu iya amfani da ƙwarewarmu, da ƙarfinmu, domin mu iya riftar zarafi da fuskantar barazana da ke akwai cikin yanayin aiki. Zaɓen hanyoyi, fusahu da dubaru da za a yi amfani da su, ya kamata ya kafu bisa a sakamakon nazarin domin a sami nasara cikin aikin neman afuwar.

**Minene ƙarfi da kasawar ƙungiyarmu ko ƙawancen ƙungiyoyinmu? Minene zarafi da barazan da ke akwai dangance da aikinmu na neman afuwa a kan wata matsala ko siyasa da muka gano?**

---

[14] Adapté de Conciliation Resources et SaferWorld. **Formation en matière de plaidoyer.** Une trousse à outils. Pp7-11

## a) Nazari na daga cikin gida – inda muke da ƙarfi, da inda muke da kasawa

Akwai fannoni a ƙalla bakwai da ake nazarinsu kamar haka: **abin da ya cancanta, abin da ya isa yarda, bada lissafi, shiri, aiki tare sauran mutane, kayan aiki, jarin kuɗi.**

Muna tattaunawa a kan wasu tambayoyi cikin yanayin kowane fanni, dangance da ƙungiyarmu ko haɗin gwiwarmu:

| Fannoni | Tambayoyin da za mu aza game da ƙungiyarmu ko haɗin gwiwarmu |
|---|---|
| ***Cancanta*** | • Da sunan wa ƙungiyarmu ke magana?<br>• Su wa za su yarda da ƴancinmu na yin magana a kan wannan mastala?<br>• Wa ki iya ƙalubalantar cancantarmu? Don mi?<br>• Yaya za mu iya inganta cancantarmu? |
| ***Yarda*** | • Wane irin hanyoyi da kayan aiki na sadarwa muke amfani da su?<br>• Ko bayanan da muke watsawa zuwa ga mutane sun isa a yarda da su?<br>• Ko ana ganin shugabannin ƙungiyarmu sun isa a yarda da su, ko suna da masaniya a kan abin da ake zance?<br>• Yaya za mu iya inganta yardarmu? |
| **Bada lissafi** | • Wa ke ɗaukar ƙuduri cikin ƙungiyarmu, ko haɗin gwiwar da muke ciki?<br>• Yaya kowa ke iya sa bakinsa cikin matakan ɗaukar ƙuduri?<br>• Ga wa maɗauka ƙudurin KFH ko haɗin gwiwarmu suke bada lissafi?<br>• Yaya ƙungiyar take tabbatar da sun bada lissafi yadda ya kamata?<br>• Yaya sauran mutane a wasu wurare suke samun bayanai, ko suke bada tasu gudummawa?<br>• Yaya muke sanas da waɗansu na cikin wata ƙungiya a kan cigaba da muka samu?<br>• Yaya za mu iya inganta bada lissafinmu? |
| ***Shiri*** | • Wace ƙwarewa ce ta can baya, za ta zama mafi tasiri?<br>• Ko kuna iya kai ga sakamakon bincike da kuke bukata domin ku tabbatar da kokowarku, ku kuma gabatar da hujjarku irin yadda za a yarda da ita?<br>• Ko kun yi tunani, ko kun shirya domin abin da aikinku zai ayyana dangance da tsaro, da hatsari bisa ga ƙungiyarku ko wasu daga cikinku?<br>• Ko kun yi tunani, kun lura da sha'anin "jinsi" yana da tamani cikin aikinku?<br>• Ko kun sansance da waɗanda abin ya shafa, da kuma mi wannan yake nufi game da cin nasara cikin aikinku?<br>• Mi ya kamata ku yi domin ku inganta shirinku? |
| **Aiki tare da waɗansu mutane** | • Ko ƙungiyarmu tana da matsayi na ƙwarai na ta yi aiki da wasu ƙungiyoyi?<br>• Minene ƙwarewarmu cikin aiki tare da waɗansu ƙungiyoyi?<br>• Ina abutar aiki mafi kyau da muka yi da waɗansu? Mi ya sa?<br>• Wace irin koyaswa muka samu da ƙwarewarmu domin mu tabbatar da cin nasara cikin hulɗoɗinmu masu zuwa? |
| **Kasancewa isassun kayan aiki** | • Ko muna da kayan aikin da muke bukata?<br>• Ko muna da mutanen ƙwarai da suke da ƙwarewa da iyawa da suka dace?<br>• Ko muna amfani da ma'akata da kayan aiki yadda ya kamata?<br>• Yaya za mu iya daidaita kayan aikinmu da tsare-tsarenmu? |
| **Tabbacin samu jarin** | • Ko akwai mataka binciken sha'anin kuɗi na ƙwarai a cikin ƙunkgiyarmu? |

| Fannoni | Tambayoyin da za mu aza game da ƙungiyarmu ko haɗin gwiwarmu |
|---|---|
| **kuɗi** | • Ko muna hangen samun sakewa cikin tsarin kashe-kashen kuɗinmu nan da shekara 2 zuwa 3?<br>• Ko muna iya tsinkayen cigaban abin da za mu samu ta fuskar kayan aiki da kuɗi nan da shekara 2 zuwa 3?<br>• Ko muna samun kuɗi daga masu zuba jari ko masu hannu da shuni da yawa? |

### b) Nazari na abin da ke waje– zarafi da barazana

A nan ma, ana ganowa da nazarin abubuwa na waje: al'amuran siyasa, tafiyarda aikin manyan ma'aikata, bada lissafi daga ɓangaren gwamnati, al'amuran tattalin arziki da al'amuran zamantakewa .

Wannan allo yana bayyana tambayoyin da suke da tasiri game da waɗannan al'amura.

| Al'amuran waje | Tambayoyin da za mu azawa game da ƙungiyarmu ko haɗin gwiwarmu |
|---|---|
| **Siyasa** | • Su wanene suke da ikon su kawo sakewar da muke biɗa, kuma su wa aka ware?<br>• Waɗanne ƙawancen siyasa ke akwai? Wace irin hulɗa ke akwai tsakanin shugabanninsu, tsakanin maɗauka ƙuduri da ƙungiyarmu?<br>• Waɗanne iri zarafi na siyasa ke akwai wanda muke iya amfani da shi domin mu cimma gruinmu – mataki, dama faɗa a ji? |
| **Manyan ma'aikatu** | • Ko ana iya saduwa da ma'aikatan gwamnati?<br>• Sassan gwamnati a ƙoli, da na cikin jahohi, sun ingantar da tsarin ikonsu?<br>• Yaya sozawa da ƴan sanda suke tafiyar da aikinsu? Ko akwai nun adalci cikin al'amarin sharia?<br>• Wane iri faɗa a ji masu zuba jari suke da bisa siyasar gwamnati?<br>• Waɗanne ma'aikatu ne na waje suke da faɗa a ji?<br>• Waɗanne ma'aikatu ne suke iya bada zarafi ga aikinmu, waɗanne n kuma suke iya hana aikinmu ya tafi daidai? |
| **Matakan bada lissafi daga ɓangaren gwamnati** | • Yaya ake aiki da sakewar da aka samu (idan lalle ana ana aiki da su ɗin)?<br>• Ko cin hanci da rashawa yana da nasaba bisa ga yadda ake ɗaukar ƙuduri? A waɗanne matakai?<br>• Ko maɗauka ƙuduri suna nuna halin a kusance su da aikin cikin haske? Yaya suke sanar da mutane da ƙudurin da suka ɗauka idan lalle sun yin haka ɗin?<br>• Ko muna samun kai ga bayanai a kan ƙudurin daban daban da aka ɗauka?<br>• Yaya ake sa maɗauka ƙuduri su bada lissafi?<br>• Yaya muke ke iya kai ga masu ɗaukar ƙuduri? |
| **Al'amuran zamantakewa** | • Ko gwamnati yana binciken dukan kafofin yaɗa labarai? Ko suna iya su soki ra'ayin gwamnati? Yaya suke wakiltar mu?<br>• Ko ƙungiyar fara hula tana da ƙarfi? Ko tana da ƴancin kanta?<br>• Ko an yardar ma ƙungiyar fara hula ta sa hannunta a cikin siyasa?<br>• Yaya maɗauka ƙuduri suke ɗaukar mu a matsayinmu na wakilan ƙungiyar fara hula, yayin da muke son mu faɗa su ji?<br>• Wa ke iya goya mana baya, wa kuma ke iya nuna mana hassada?<br>• Yaya ake amfani da sadarwa ta yanar gizo cikin aikin ƙungiyar? |
| **Al'amuran tattalin arziki** | • Yaya matsalar da muke warwarewa take da nasaba bisa ga tattalin arzikin ƙasa? Wace riba ake samu ta fannin tattalin arziki? Ina tamaninsu?<br>• Ina nasabar matsalar dangance da yadda mutane suke samu kayan aiki, hilaye da gonaki, da hanyoyin sarrafa abubuwa?<br>• Yaya halin tattalin arziki na gaba ɗaya yake da nasaba bisa yadda muke aiki, da kuma bisa halin rayuwar matalauta?<br>• Wace irin hulɗa ce gwamnati yake da tsakaninsa da masu zuba jari idan akwai hulɗar? |

| Al'amuran waje | Tambayoyin da za mu azawa game da ƙungiyarmu ko haɗin gwiwarmu |
|---|---|
| | • Waɗanne hanyoyin warware matsala ta fannin tattalin arziki ke akwai? |

### c) Allon nazarin ƘKZB

Bayan da kun lisafa al'amuran cikin gida da na waje, sai ku gabatar da allon ƘKZB, ku tambayi mahalarta taron su faɗi wurin da ake da ƙarfi, da wurin da ake da kasawa, da zarafi, da barazana, ta wurin amfani da tambayoyi da aka aza cikin kowane ɓangare na allon.

| Inda ake da ƙarfi | Inda ake da kasawa |
|---|---|
| Waɗanne al'amura na ƙwarai ƙungiyarku take da, waɗanda ke da muhimmanci cikin aikinku? | Waɗanne al'amura ne ke cikin ƙungiyarku da suke iya hana maku yin aiki? |
| **Zarafi** | **Barazana** |
| Waɗanne al'amura ne ke cikin al'aumma (waɗanda ba sa cikin ƙungiyarku) da suke iya kyatata aikinku? | Waɗanne al'amura ne ke cikin al'umma (waɗanda ba sa cikin ƙungiyarku ba) da suke kawo cikas ga aikinku? |

## 2.9 Farilai na farko na neman afuwa

Idan ana son a ci nasara cikin neman afuwa, akwai hali da akidar ya kamata a kiyaye. Akwai kuma farilai da ya kamata ƘFH ta sani, ta raba, kuma ta kiyaye; ko kuma su abukan ƙanwancen ƙungiyoyi. An taƙaita waɗannan farilai kamar haka[2] :

- **A zama da adalci zuwa ga muhukunta na ƙasa**

In banda wata togiya, suna aiki da sahihanci, suna da azanci, kuma suna son su yi aikin ƙwarai. Aikin ƘFH shi ne su sanas da su yadda ya kamata bisa ga abin da suke gani daidai ne.

- **A guje ma rashin gaskiya**

Gwamnati da masu tafiyar da siyasa na iya yin kuskure, amma ba cikin dukan fannonin aiki ba. Matakin siyasa da ƘFH hula suke yawan zargi, kullum shi ne babban begensu domin su kawo sakewa mai ginawa cikin al'umma.

- **A iya ganewa**

A yi kamar an ɗauki matsayin hukuma. A nemi a gane matsala/matsalolinta, da famarta, da hangenta, da kuma gurinta.

- **A yi komi cikin abuta**

Ba ya kamata ba a ce sai in ƘFH na bukatar taimako ne kaɗai take kusantar hukuma ba. Ya kamata su riƙa hulɗa da junansu dukan tsawon shekara, kuma kowace shekara.

- **A iya lissafi**

A san da cewa akwai bambancin ra'ayi da ya cancanta. Ba ya kamata ƘFH ta yi ta nuna barazana ba.

- **A nuna jinƙai**

Kasawar hukuma na ta yi abin da ƘFH ke so, na iya zama laifinta na rashin shiri, gabatarwa da bin sau-da-ƙafa na aikinta. Kowace hukuma ta san da cewa ƴan ƙasa suna furta ra'ayinsu wurin zaɓe.

- **A nuna halin ginawa**

Babu wanda ke son a yi ma faɗa, ko a haddabe shi, ko a yi masa wa'azi. Haka kazalika hukuma. Yawanci lokaci irin wannan ba ya gyarawa. Abin da ya kamata shi ne a gabatar da wata sabuwar hanya, ba wai a yi ta mugun zargi ba zuwa ga maɗauka ƙuduri.

---

[2] *Traduit et adapté de : A Guide for the Powerless — and Those Who Don't Know Their Own Power; Samuel Halperin, Institute for Educational Leadership, Washington, D.C., 1981*

- **A san abin da ke yiyuwa, a kuma nace**

Ya kamata ƘFH ta tuna da cewa ko da akwai gardama a kan wasu dokoki, ana iya a sasanta daga baya. Ba dole ba a ce, ala tilas sai kowa ya sami biyan bukata. Wani lokacin ana ganin cewa ƘFH tana tafiya sannu-sannu, amma tana nacewa cikin sanin abin da ke yiyuwa.

- **A zama ɗan adawa na ƙwarai**

Ya kamata ƘFH ta yaƙi matsaloli, da miyagun matakai, amma ba mutane ba.

- **A sami bayani**

Ya kamata ƘFH ta yi aikin neman bayanai a ko da yaushe. Bai isa ta ce abin da take so hukuma ta yi, shi ne kawai ta yarda da ra'ayinta ba.

- **A zama abin yarda**

Idan aka yi alƙawarai, to a cika su. Idan ƘFH ta ce ma hukuma za ta yi wani abu, to sai ta yi haka ɗin.

- **A auna girman matsalolin**

An nemi a yi jifa da tsarin dokoki da yawa, ba su taɓa tabbata dokoki ba. Kenan ba ya kamata ƘFH ta yi zargin masu kafa dokoki ba a kan duk kowane tsarin doka da aka gabatar da shi ba, kuma kada ta tsorace har sa'arda ta ji cewa an tabbatar da wata doka.

- **A zama da nuna godiya**

Ya kamata ƘFH ta tuna da cewa, idan aka sami nasara, kowa na son a ce shi ne. "nasara tana uba dubu, amma kasawa marainiya ce" in ji wani karin magana. A gode ma hukuma a ƙalla domin dukan abin ƙwarai da suka yi; ko da ma ƘFH ta tambaye su mi ya sa suka yi kuskure nan da can. Ku sanas da su cewa ƘFH tana lura sosai da abin da suke yi. Ana bukatar a yaba abin da aka da kyau, ko ma a ce dole ne.

- **A zama da amfani**

Abin da ƘFH ke iya yi domin ta sauƙaƙa aiki hukuma yana ɗaukar tsawon lokaci.

- **A yi aiki cikin naciya**

Ya kamata ƘFH ko ƙawancensu, su san da cewa aikin neman afuwa yana ɗaukar lokaci mai tsawo da ƙoƙari mai yawa.

## 2.10 Dubaru da kayan aiki na neman afuwa

Ana bukatar a shirya dubara ingantaciya domin a ci nasara cikin taron gangami na neman afuwa. Ya kamata a shirya wannan dubara tare mutane, kuma a yi amfani da sakamakon nazarin ƘKZB.

Nanzarin yanayin cikin gida da na waje, na sa a san abin da za a yi dangance da matsalar neman afuwa. Kafin a shiga cikin aiki gadan gadan, ya kamata ƘFH, ko ƙawancensu ya aza tambayoyi game da yadda za a tafiyar da aikin. Dangance da kowane fannin bayanai, ya kamata ƘFH ta sami amsoshin tambayoyi waɗanda suke daidai ko waɗanda suke kusa da yadda halin ya kasance.

Wannan tambayoyi sun zama jagora da ake iya bi, domin a taimaki ƙungiya ta ga irin bayanan da take bukata, da za su taimaka wajen shimfiɗa dubara mai kyau, da kuma masamman zaɓen kyakkyawan matakai.

| Irin bayanan da za a nema | Tambayoyin da ƙungiya ko hadin gwiwa za su aza |
|---|---|
| Matsala | • Ko matsalar mai tsanani ce ?<br>• Ko matsalar ta gaugawa ce?<br>• Ko akwai bukatar neman afuwa ? |
| Abin da matsala take ayyanawa | • Yaya matsalar take shafar talakawan da ƘFH take ga taimaka ma?<br>• Ko matsalar tana shafar wasu gungun mutane ? Idan haka ne, su wa ne, kuma yaya take shafar su?<br>• Ko kuna da isassun bayanai? |
| Tushen matsalar | • Wane aiki siyasa da tabi'un gwamnati (a wurare da cikin ƙasa gaba ɗaya) suke yi ?<br>• Minene aikin eklisiyoyi da sauran gungun mutane suke yi?<br>• Minene gudummawar al'amuran al'adu da na muhalli?<br>• Ko talakawa suna sa bakinsu cikin ɗaukar ƙuduri? |
| Hanyar warware matsalar da za a bi | • Wace shawara ƘFH take badawa?<br>• Minene riba da illar hanyar?<br>• Ko ƘFH na iya tabbatar da matsayi/ra'ayinta?<br>• Ko shawarwarinta masu yiyuwa ne?<br>• Yaya za ta iya auna cin nasara?<br>• Ko kun san yadda sakewa za ta abku? |
| Masu faɗa a ji | • Wa ke da ikon kawo sakewa?<br>• Gwamnati ne, eklisiyoyi ne, ƙungiyoyin al'umma ne, ko shugabannin gari?<br>• Ko ƘFH na iya saduwa da su?<br>• Ko suna shirye su ƙarɓi mutane?<br>• Ko sun yarda da cewa suna da wajibin sake abubuwa?<br>• Ko lalle suna iya yin wani abu domin su taimaki ƘFH? |
| Abukan aiki da suke aiki bisa ga matsalar da aka gano | • Ko ƘFH na iya aiki tare da su?<br>• Ko aikinsu yana da inganci?<br>• Mi ake bukatar sakewa?<br>• Ko akwai mutanen da babu ruwansu da matsalar, amma ƘFH na iya shayo kansu domin su taimaka mata |


| Irin bayanan da za a nema | Tambayoyin da ƙungiya ko haɗin gwiwa za su aza |
|---|---|
| Hatsarin da ke tare da aikin neman afuwa | • Minene hatsarin da ke akwai cikin aikin neman afuwa?<br>• Mi kuka yi domin rage hatsarin?<br>• Wane irin hatsari zai abku idan kuka ƙi fuskantar matsalar ta wurin neman afuwa?<br>• Wane irin dalilai ne kuke tsammani suka haddasa matsalar, da kuma yaya kuke ganin za ta shafi ma'ikanta, da kuma ƙarfin aikinku? |
| Matakan da za a bi | • Waɗanne matakai ne suka fi dacewa?<br>• Ko ƘFH tana jin sauƙin amfani da matakan?<br>• Ko atakan sun nuna inganci can baya?<br>• Ko akwai wasu matakai daban da ƘFH ke iya gwadawa?<br>• Ko ƘFH tana da isassun kayan aiki da ƙwarewar da domin ta iya aiki da su yadda ya kamata? |

## 2.11 Matakai da kayan aiki na dubarar neman afuwa

Da shike neman afuwa yana bin matakai, ba abin da ake yi sau ɗaya ba, hanyar tafiyar da hidimomi mai inganci, shi ne a shimfiɗa "dubarar neman afuwa" wadda za a aiwatar da ita dukan tsawon lokaci tare da hazaƙa da nacewa. Matakan shimfiɗa dubarar neman afuwa sun bambanta dangance da waɗanda suka ƙirƙiro su, amma abin da ta ƙumsa kusan iri ɗaya ne.

An shirya wannan tsari mai matakai tara, domin a tabbatar an yi amfani da dukan manyan abubuwa, cikin shiri da aiwatar da dubarar neman afuwa. Tsari ne da aka yi domin a tabbatar da an yi amfani da manyan al'amura da suke ƙarfafa aikin ƘFH, da kuma domin a gano da guri, da mutanen da aka nufa na kan gaba, domin a bunƙasa tasirin aikin neman afuwa, ta wurin amfani da kayan aiki ƴan kaɗan da ke akwai.

**Hoton kwatancin dubarar neman afuwa mai mataki takwas (8)**




- **Mataki na 1 : A sansance da matsalar ko dalilin neman afuwa**

Yana da muhimmanci tun daga farko a sansance kuma a gane da matsalar ko dalili, tamkar wani tunani da al’umma ko ƘFH take so a fuskanta ta wurin neman afuwa. Ana iya yin wannan nazari da kayan aiki iri biyu masu muhimmanci.

- ***Yadda ake kwatanta matsaloli da siffar ice***

Kwatanta matsaloli da siffar ice, yana zance a kan gano da miyagun sassa (illa) na wani hali, yana kuma bayana ma'amalar da ke akwai tsakani mafarin matsalar da abin da take ayyanawa.




| Sashen icen | Matsala | Bayani |
|---|---|---|
| **Sayu** | Dalilai(mafari) masu zurfi na matsalar | Su ne dalilai da suka zama mafarin matsalar, kuma su ne ya kamata a fuskanta. Dalilan na iya iya fitowa daga al'amarin zamantakewa, tattalin arziki, da siyasa. Yawanci lokaci suna kafe cikin addini (bangaskiya), tsare-tsaren da ba a shirya su daidai ba, da ba sa aiki da kyau. |
| **Gindin icen** | Babbar matsala | Matsala ce da take tsakiya, da ake gani. |
| **Rassa** | Illar da matsalar take ayyanawa | Illar ta bambanta da dalilai, ko alamun matsalar. Illa shi ne abin da matsalar ke haddasawa, ita kuma illar dalilan ne ke zuga ta. |

Yawanci lokaci, masu aikin cigaba har, har ma da ƘFH suna neman su kawasda illa ko sakamakon matsala, abin su nemi kawas da dalilanta.

Alhali idan aka datse rassan ice, ba tare da an datse sayunsa ba, sayun za su ci gaba da shayarda gindin, sai kuma rassa su ci gaba da girma.

- ***Yadda ake furta matsalar neman afuwa***

Ma'ana ko furci matsalar neman afuwa na da sassa huɗu.(4):

1. Babbar matsala ta tsakiya;
2. Dalilai masu zurfi na matsalar;
3. Sakamako da illa da matsalar da haddasawa (masu rasawa ko masu amfana da kasancewa matsala);
4. Hanyoyin warware matsala da aka bada shawararsu.

| |
|---|
| **Yadda ake furta neman afuwa**<br><br>**Babbar matsala**<br>……………………………………………………………………………………………………………………<br>……………………………………………………………………………………………………………………<br><br>**Dalilan matsalar masu zurfi**<br>……………………………………………………………………………………………………………………<br>……………………………………………………………………………………………………………………<br><br>**Sakamako/illar da matsalar ke haddasawa**<br>……………………………………………………………………………………………………………………<br>……………………………………………………………………………………………………………………<br><br>**Hanyoyin warware matsalar da aka bada shawararsu**<br>……………………………………………………………………………………………………………………<br>…………………………………………………………………………………………………………………… |

- **Mataki na 2 : Ƙayyade manufa da gurin neman afuwa**

Shirya dubaru da ayukan neman afuwa za ya zama da sauƙi idan KFH za ta iya ƙayyade manufa da gurin da take son ta cimma.

***Manufar neman afuwa*** sakamako ne mai dogon zango da KFH take son ta cimma. Tana bayyana sakewar da KFH ke son ta gane ga wasu mutane ko al'umma gaba ɗaya. Sakamako ne mai dogon zango na ƙoƙarinta da hangenta na kawo sakewa

***Guri*** «abin da ake son cimma » cikin gajeren zango wanda zai taimaka ga cimma manufa mai dogon zango. Sakewa ta masamman ce KFH ke son samu wadda za ta taimaka ga cimma manufarta. Dubarun neman afuwa suna da guri daban daban da suke taimakawa zuwa cimma manufa da hangen gaba ɗaya.

***Yadda guri na ƙwarai yake***

Yana da muhimmancin a san da cewa ko da neman afuwa na samun abubuwa da yawa, ba zai iya samun dukan abin da yake so ba; kenan ya kamata guri na ƙwarai ya zama KACYL(Kayyadadde, Mai Aunuwa, Mai Cimmuwa, Mai Yiyuwa, cikin Lokaci):

- **Kayyadadde** : ya kamata a ƙayyade shi yadda ya kamata, an san ainahin abin da ake biɗa a samu.
- M**ai Aunuwa** : domin a iya ganin tasirin aikin neman afuwa.
- **Mai Cimmuwa** : kenan ya kamata a rage faɗin rai, domin a guje ma kokowa cikin wurare da yawa a lokaci guda, idan ana son a sami sakamakon mai inganci
- **Mai Yiyuwa** : ya kamata ya yi daidai da yanayin da ake ciki, wato ya kamata gurin ya lura da ƙarfin waɗanda ke nan, tunani da muradin waɗanda abin ya shafa da wata dama da yake hanawa.
- **Cikin Lokaci**: yawanci lokaci , lokacin da ake iya cimma gurin neman afuwa, ana ƙayyade shi cikin shekara 1 zuwa 3.

| Misalin gurin nema afuwa | |
|---|---|
| **Misali maras kyau** | **Misali mai kyau** |
|  Bunƙasa yanayin siyasar fannin kiyon lafiya da ya shafi haifuwa |  A sa gwamnati ya aza doka/siyasar ƙasa da ta shafi kiyon lafiya da haifuwa, nan da shekara uku. |
| |  A sa ƴan majalisa su sauya ayoyin doka a, b, c, d na dokar ƙasa bisa kiyon lafiya da ya shafi haifuwa. |
|  Bunƙasa HKLJH cikin gunduma |  A ƙara kasafin kuɗin ƙasa da na shekara da kashi 15% wanda ake sawa cikin kiyon lafiya da ya shafi haifuwa, cikin gundumar Sagabari daga shekara 2020/2021 |
|  A ƙirƙiro kyakkyawan yanayi domin nakasassu ta fannin kiyon lafiya da ya shafi haifuwa |  A sa gwamnati ya shirya dubara tarbiyya ta ƙasa domin nakasassu daga nan zuwa shekara 2025. |

- **Mataki na 3 : A yi nazari a kan mutanen da aka nufa da neman afuwa**

Da zarar an sasance da matsala, da manufa, da guri na neman afuwa, za a yi ƙoƙarin neman afuwa domin a shayo kan **mutanen da aka nufa, wato su wanene za ku nemi afuwar wurinsu**. Wannan mataki yana da muhimmanci sosai, da shike shi ne zai nuna cin nasara da ingancin dubarar neman afuwa ta ƘFH, saboda domin a sami sakamakon da ake so, sai an tambayi waɗanda suke da ikon bada sakamakon. Saboda haka, sai an gwada mutanen da aka nufa iri biyu, wanda suna cika ajin juna:

- **Mutanen da aka nufa kai tsaye** : su ne maɗauka ƙuduri da suke da ikon su sake, su ƙarfafa, su gyara wata siyasa, wata doka, wata ka'ida, wata yarjejeniya, wata al'ada, ds. Ƙudurin yana shafar gurin neman afuwa kai tsaye. Waɗanda aka nufa na farko, su ne waɗanda suke kawo sakewar da ƘFH ke so ta cimma ta wurin ayuka neman afuwa, inda ma'akatun gwamnati suke gabatar da su (gwamnatin ƙasa), da ƴan majalisar hukumomi a matakai daban daban.
- **Mutanen da aka nufa amma ba kai tsaye ba**: su ba sa ɗaukar ƙuduri game da kawo sakewa, amma suna iya faɗa a ji sosai cikin ƙudurin siyasa, da shike ra'yinsu yana da ƙarfi bisa ga mutane a mataki na farko. Mutane ne masu kyautata sakewa, ko su hana ta. Wannan gungun mutane suna da yawa, inda akwai: mashawartan masu ɗaukar ƙuduri, Magatakardu, ko shugabannin jam'iyyun siyasa, shugabannin sozawa ko ƴan sanda, masu zuga wasu, kafofin yaɗa labarai, ƙungiyoyin ma'aikata, da mutane masu galihu da samun yarda.

Da shike wani lokaci babu isassun kayan aiki domin tafiyar da neman afuwa, yana da muhimmanci, a fi maida hankali bisa mutane guda guda, da gungun mutane ko ma'aikatu waɗanda suke da ƙarfin kawo sakewar da ake so. Sansancewa da waɗanda aka nufa zai tamaka ma ƘFH ta shirya tsarin dubarunta na neman afuwa, da kuma zaɓen hanyoyi da fusahohi da suka fi dacewa.

- **Mataki na 4 : A kafa ƙawance da haɗin gwiwa na neman afuwa**

Aikin neman afuwa cikin ƙawance ba dole ba ne, amma ƙawancen mutane ko ƙungiyoyi da suke wannan aiki na sa a sami biyan bukata fiye da in ƙungiya guda ce. Wannan ya nuna cewa yana da muhimmanci ga ƘFH ta duba ta gani idan da ya kamata ta sa kuɗi da ƙarfinta. Aiki cikin ƙawance yana iya zama da riba ta fannin raba kayan aiki tare da waɗansu. (ko kuɗi ko ma'aikata).

Duk da haka wasu gungun mutane ko mutane guda guda, na iya zama tamkar "abukan aiki" da suke tallafawa, ko kuma ƴan adawa da suke adawa da dalilin abin da ƘFH take ƙoƙarin karewa. Sansancewa da irin waɗannan mutane na iya zama da amfani domin gano da matsalolin ko ƙiyaya da ƘFH ke iya fuskanta tare da sanin asulinsu.

| Sansancewa da sassan da abin ya shafa | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|
| Sashen da abin ya shafa | Yadda suke | Muradi dangance da matsalar | Matsayi bisa ga matsalar (babban iko + ƙaramin faɗa a ji, ƙaramin iko + babban faɗa a ji) | Iya ƙarfafawa da faɗa a ji | | |
| 1. | | | | Babba | Madamanci | Ƙara mi |
| 2. | | | | | | |
| 3. | | | | | | |
| 4. | | | | | | |
| … | | | | | | |

A ƙarshe, banda haka **« abukan aiki » da « ƴan adawa »** na ƘFH, akwai mutane da yawa ba su da wani ra'ayi a a kan darasin da ake zance a kai. Suna iya zama **«ƴan ba ruwana ».** Wasu na iya zama abukan aiki da ƴan adawa gaba daya. Dangance da halin da ake ciki, misalin wani sabon cigaba cikin ƙasa ko cikin al'amura, waɗannan mutane suna iya su zama abukan aiki ko abukan gaba ta dalilin ƘFH.

**Abin da ya kamata ƘFH ta yi:**

- Ta yi nazari matsayin waɗanda suke jiagajigai cikin waɗanda ke aiki tare;
- A sansance da waɗanda suka fi iko ko galihu cikin siyasa, tattalin arziki da zamantakewa;
- A yi nazarin hatsari/riba da mutanen da kuka nufa ke iya samu, indan ta goya maku baya;
- A san su wanene ƴan ba ruwana, da kuma mi ya sa haka.

| **Fasalin waɗanda abin ya shafa(Ɓangare daban daban)** | | |
|---|---|---|
| **Matsayi** | **Suna** | **Tambayoyi** |
| Abukan aiki | Su wanene abukan aiki? | Wane muradi gare su na goyon bayan dalilin neman afuwa?<br>Ko yana da amfani a kusance su ta wurin kafa ƙawance, ko haɗin gwiwa, ko kuwa kowa ya riƙe nasa saƙo? |
| Ƴan adawa (abukan gaba) | Su wanene manyan ƴan adawa | Ina hujar gaba da su?<br>Yaya za a kuzarantar da su, a kuma shayo kansu? |
| Abukan aiki & Abukan gaba | Su wanene abukan aiki da kuma ƴan adawa gaba ɗaya? | Mi ya sa suke nuna wannan hali ?<br>Yaya za kuzarantar da su, a kuma shayo kansu? |
| Ƴan ba ruwana | Su wanene ? | Mi ya sa suke nuna wannan hali ?<br>Yaya za a kuzarantar da su, a shayo kansu, a kai su ga goya mana baya ? |

Wannan fasali yana sa ƘFH ta yi nazarin a kan kowane ɓangare, masamman masu goyon bayanta. Wannan bai isa ba, dole sai ƘFH ta shiga cikin aikin ƙirƙirowa da tattalin abukan aiki masu dubara da faɗa a ji. Ana yin wannan ta wurin bin matakai.

| **Matakan ƙirƙiro abukan aiki da tattalin ƙawance** | |
|---|---|
| **Mataka** | **Abubuwanda ake yi** |
| **Mataki na 1** | A sansance da abukan aiki<br>- Mutane: guda guda ko gungun mutane<br>- Kungiyoyi: Ƙungiyoyi / Ma'aikatu /... |
| **Mataki na 2** | A yi nazari a kan abukan aiki domin a ƙara sanin su (sunansu, aikinsu, inda su sa gaba, cibiyar ma'aikatarsu, fannonin da suke aiki ciki, muradinsu game da al'amarin, shahararsu, faɗa a jinsu, ds.) |
| **Mataki na 3** | A sa abukan aikin su ji marmarin gurin neman afuwar, a shayo kansu domin su goya ma dalilin baya |
| **Mataki na 4** | A ƙayyade wajibi da aikin kowane abokin aiki. Wa zai yi mi? Yaya? Ƙaƙa? Yaushe? Da waɗanne kayan aiki? Ana bada shawarar ƘFH da suke tafiyar da aikin, su shirya kuma su sa hannu a kan yarjejeniya da haɗin kan abukan aikin. |
| **Mataki na 5** | A kula, a yi tattalin hulɗa da abukan aiki: a tuna da manyan farilan aiki tare. A sake duba farilan in ana bukata. A riƙa yin taruwanni na auna aikin kansa. |
| *Source : Atelier International - Oxfam ; Planification stratégique du plaidoyer* | |

- ## Mataki na 5 : A shirya saƙonnin neman afuwa

Saƙo furci ne tsararre, mai iya shayo kan mutane game da gurin neman afuwa, inda ake bayyanawa a sarari abin da ƘFH take so ta yi, don mi, da kuma ƙaƙa. Ana shirya saƙonnin neman afuwa domin sanas, a shayo kan mutane, a kuzarantar da mutane domin su ɗauki mataki.
A wannan mataki ana bukatar waɗannan tambayoyi:

- Bisa ga gurin da ake da shi, wane irin saƙonni ne ke iya shayo kan mutanen da aka nufa na farko?
- Ko ana bukatar wasu saƙonni daban domin waɗanda aka nufa na biyu? Waɗanne suke sa a sami matsayi na ƙwarai wurin kafofin yaɗa labarai, ko a yi suna, inda mutane suke yaɗa saƙon?

Ta wurin saƙonni masu iya shayo kan mutane, ƙarfafa sadarwa yana da muhimmanci, idan ana so a ci nasara cikin gangamin neman afuwa. Bayani, yana da muhimmanci cikin neman afuwa, ana bukatar ya amsa wasu manyan tambayoyi:

***Wa? Ya yi/ zai yi…mi? Yaushe? Ina ? Don mi?, Da wane tasiri? Don wane sakamako?***

Abin da saƙon ya ƙumsa ba shi kaɗai ba ne abu mai muhimmanci cikin isar da shi, amma masamman akwai wasu al'amura da ba na a faɗa ba ne, kamar:

- Yarda zuwa ga ƙungiyar;
- Mutuncin wanda yake isar da saƙon;
- lokaci, lokacin isar da saƙon, (ko kuma wuri).

Abin da saƙo ya ƙumsa da fasalin saƙon zuwa ga maɗauka ƙuduri, na bukatar ya nuna masu (su wa ?), yadda ayukan (mi ?) za su iya ƙarfafa matsayinsu cikin siyasa da zamantakewa, ko a ƙalla darajarsu cikin tunanin al'umma da cikin ƙasashe. Banda wannan, ya kamata saƙonni su bada hujjojin da suka isa a yarda da su (abin da saƙon ya ƙumsa), ya kuma fiddo a sarari, ko daga ɓoye, ko mi ke riƙe da ƙungiyar.

Saƙon neman afuwa na da manyan sassa huɗu (4) kamar haka:

Furcin saƙo → Tabbaci (abin da ke faruwa) → Misalai → Abin da ake fatan a yi/ko ake so

Ya kamata duk wani saƙon neman afuwa, ya ƙumshi a ƙalla waɗannan abubuwa huɗu.

**Shawara uku domin shiryawa da gabatar da saƙonnin neman afuwa[1]**

1. **A gabarar da saƙo ga mutanen da aka nufa ta wurin amfani da hanyoyin sadarwa da yawa cikin lokaci mai tsawo.**
   Saƙonnin ba za su iya karɓuwa ba, ko su jawo hankalin mutane ba cikin yini guda; maimaitawa tana da muhimmanci. Nacewa tana da nata muhimmanci, saboda bai kamata a sake saƙon ba, muddar ba mutane sun "karɓe" shi ba. A isar da saƙo cikin kamani iri-iri, da kalmomi daban daban, domin kada ya zama abu guda da zai dami mutane.

2. **A bincika a gani idan saƙon ya isa ga mutane ta hanyar da aka yarda da ita, a idanun waɗanda aka nufa.**

   Hanyar isar da saƙon tana da muhimmanci (wani lokaci mafi muhimmanci) fiye da saƙon karan kansa. Misali, idan KFH tana son ta isar da saƙo cikin jarida, to ya kamata ta yi amfani da jaridar aka fi karantawa, aka kuma fi darajantawa.

3. **A shirya saƙon da mutane za su gane. Wato a yi amfani da sanfarin (kalmomi ko harshen) mutanen da aka nufa**
   A guje ma amfani da kalmomi irin na fusaha, ko irin na wanin gungun mutane. Idan kuna amfani da alluna da hotuna, to sai ku yi su a sauƙaƙe, da sarari, da sauƙin ganenwa. Ku yi amfani da kalmomi ko sheɗaru masu ɗauke da hotuna na ƙwarai, masu jan hankalin mutane, amma ba masu kawo mugun tunani ba.

- **Mataki na 6 : A zaɓi hanyoyin sadarwa**

Takardu da ƴan littattafai, sanarwar irin ta talla, ko a rubuce cikin jarida, gabatarwa a magance gaban mutane cikin taruwanni, hira cikin radiyo, cikin tele, sanarwai.

| Fasalin saƙo dangance da mutanen da aka nufa | |
|---|---|
| **Mutanen da aka nufa** | **Fasalin saƙon da za isar** |
| **Maɗauka ƙuduri na farko da mutane masu faɗa a ji** | • Tarwuanni na fuska da fuska cikin an tsara ko cikin ba a tsara ba, wasiƙu, takardu masu nuna abin da ke faruwa, hotuna, rubutawa cikin jaridu, tattanawa cikin radiyo da tele, gajerar gabatarwa cikin bidiyo, cikin na'ura mai ƙwaƙwalwa, hotuna da ake halbawa kan bango |
| **Ƙungiyoyi** | • Taruwanni tare da shugabanni, da ma'aikata, takardu masu nuna abin da ke faruwa, hotuna, gabatarwa da na'ura mai ƙwaƙwalwa, hotuna da ake halbawa kan bango, taruwanni na bada bayanai. |
| **Kafofin yaɗa labarai** | • Sanarwa/taron manema labarai, taron da ake bazawa cikin kafofin yada labarai, takardu masu nuna abin da ke faruwa, wasiƙu, hotuna ko kwatance. |
| **Zuwa ga taro mai yawa** | • Rubutu bisa ƙyalle, abubuwan saidawa, gabatarwa a cikin taruwannin cikin al'umma, sanarwa da ake damɓalawa, takardu masu nuna abin da ke faruwa, muhawara cikin radiyo, ko tele, sanarwai, rubutawa cikin jaridu. |

Yana da muhimmanci a shirya kuma a wallafa abin yaɗa bayanai, da bunƙasa ƙungiyarku, da matsalar da kuke neman afuwa a kanta cikin kalmomin da suka dace, masu sauƙin ganewa ga mutanen da kuka nufa.

- **Mataki na 7 : Tanada kayan aiki domin neman afuwa**

In babu kayan aiki, ƙoƙarin neman afuwa ba zai ci gaba ba. Ci gaba da wannan ƙokari cikin dogon zango na bukatar lokaci da ƙarfi, domin a samo kuɗi ko wasu kayan aiki da za su tallafa ma aikin. Alahali, shahara, da niyya, da hangen samun sakewa ga mambobin ƘFH da ƙawancensu, tushe ne mai muhimmanci. Yaya za a iya samun kayan aikin da ake bukata domin a tafiyar da aikin neman afuwa?

Ana iya amfani da hanyoyin biyu:

- **Guddumawa daga mutanen wuri**, inda akwai tarbace, gudummawa ta kayayaki, shaharar da ke akwai, faɗa a ji na ƘFH, sana'u masu kawo kuɗi, wanda dukan waɗanda suke cikin aikin neman afuwa za su kawo.
- **Gudummawa daga waje** ta ƙumshi kyauta, gado, tallafi, neman taimako, gudummawa daga ma'aikatu, daga ƙungiyoyi, masu zuba jari da ƘFH ta yi kira gare su.

Irin kayan aikin da ake so, su ne: kuɗi, ƙwararrun ma'aikata, gudummawa ta kayayaki, shahara, taimako ta fannin tafiyar da aiki, wurin yin taruwanni, da takardu da sauran kayan aiki.

Yana da muhimmanci, ƘFH ta shirya kasafin kuɗi mai yiyuwa, wato yawan kuɗin da

tsarin neman afuwa ke bukata, waɗanda za a samu da waɗanda za kashe. Ya zama hanyar bincike, taɗi, da sasantawa tsakanin masu tafiyar da aikin da na waje. Yana sa nemi daidaici, iya cika aiki, tsakanin kayan aiki da ake da su, da ayukan da ake yi, cikin aikin cimma gurin neman afuwa.

- **Maaki na 8 : A shirya tsarin aikin neman afuwa**

Yanzu, ƘFH tana dukan abubuwan da take bukata domin ta shirya tsarin aikin neman afuwa, da hidimomin da suka dace domin ta cimma gurinta da ta ƙayyade, da kuma kawo sakewar da ake so. Tsarin aikin neman afuwa yana shimfiɗa zarafi domin kowace hidima, yana kuma ƙayyade wanene ke da nauyin aiwatar da su. Idan ana son a ƙayyade hidimomin da suka dace, to yana da muhimmanci a lura da sakamakon matakai na 1 zuwa 7.

**Misalin tsarin aikin neman afuwa**

Kungiyar da ke aikin neman afuwa :……………………………………………………………………………………

Kungiyoyi mambobin haɗin gwiwa/ƙawance :……………………………………………………………………………
……………………………………………………………………………………………………………………………………

Manfar neman afuwa :……………………………………………………………………………………………………………

Guri daban daban :

| Guri | Sakamakon da ake jira | Waɗanda aka nufa | Hidimmomi da dubarun tafiyar da su | Kayan aiki | Shugabanni | Lokacin da aka ƙayyade | Ƙalubalan da ake jira |
|---|---|---|---|---|---|---|---|
| #1 | | | 1.1. | | | | |
| | | | 1.2. | | | | |
| | | | 1.3. | | | | |
| #2 | | | 2.1 | | | | |
| | | | 2.2. | | | | |
| | | | 2.3. | | | | |
| #3 | | | 3.1. | | | | |

- **Mataki na 9 : ya shafi sauran dukan matakai: Bin sau-da-ƙafa da auna aikin neman afuwa**

Kafin a fara duk wani aiki na neman afuwa, yana da muhimmanci a ɗauki ɗan lokaci a shirya yadda ƘFH za ta auna tasirin hidimomin da za a aiwatar da su. Auna sakamako da tasirin neman afuwa ya fi ƙayyade cin nasara proje “ mai maida hankali ga bada kulawa” wuya

Bin sau-da-ƙafa hanya ce ta bada bayanai, wadda manufarta ita ce ta sauƙaƙa ɗaukar ƙuduri, ta inganta aikin da ake yi, da bada dalilin da ake amfani da kayan aiki. Yana yin abubuwa iri uku:

1. **Bada bayanai**: bada bayanai a kan abin da ke faruwa;
2. **Yabawa:** alamu, kyakkyawa da miyagun abubuwa da ake gani cikin aiwatar da hidimomi, da gyaran da aka yi cikin tafiyara da aikin;
3. **Aunawa:** a yi nazari mai zurfi na matsalolin da za a warware, a kuma zartas game dangance da guri daban daban da aka ƙayyade tun farkon aikin.

**a) Bin sau-da-ƙafa**

Lura ne da nazari a kan kari, ko da yaushe na yadda ake tafiyar da hidimomin da aka tsara cikin tsarin aikin neman afuwa, domin a tabbatar da cewa kayan aiki da hidimomi suna iya sa a cimma sakamakon da ake jira, da kuma gyara su. Ana kiran wannan sa ido da lura.

**b) Auna aiki**

Kwatanci ne tsakanin abin da aka hanga, da abin ya tabbata a ainahi cikin wani aikin neman afuwa, domin a san ko wata hidima ko hidimomi, sun sa a cimma gurin da aka ƙayyade tun daga farko. Yana bada damar a ga inganci da cikawar hidimomin da aka tafiyar da su.

Bin sau-da-ƙafa bincike ne na ko da yaushe, amma auna aiki ana yin shi lokaci zuwa lokaci. Ana yin su duka ta wurin amfani da sakamako masu alamu da aka tsaida.
Ana iya auna aiki a matakai da yawa: matakai, abin da da aka samu, sakamako da tasiri.

- **Auna matakai da abin da aka samu**

Shi ne abin da ke rubuce da abin da aka yi cikin neman afuwa. Yana sa a iya bada amsa ga tamabaya kamar haka: Yaya wannan ya faru? Ko darasin da aka koya daga wannan hali yana sa a inganta tafiyar da aikin neman afuwa da ake yi, ko shirin wasu ayuka da za a yi nan gaba: Yaya abin ya faru? Auna aikin yana lura da al'amura kamar haka:

- Dubarar aiki : hanyar ta gaba ɗaya, da hanyoyi na masamman da aka zaɓa na tafiyar da aiki, har ma da dubarar neman afuwa (shirya ta). Ko su nuna inganci? Ko sun dace? Ƙaƙa suka yi amfani da hanyoyin isar da saƙo?
- Kayan aiki (da suke shiga), ma'aikata, shiga da fitar kuɗi, shiga da fitar bayanai (yawansu, ingancinsu, zarafi) , shiga da fitar kaya, taimako ta fannin fusaha.
- Hidimomi: ko hidimomin da aka tsara, an tafiyar da su yadda aka tsara, (bisa ga fasalinsu, lokiacin aiwatar da su, da sakamakon da ake jira)? Idan ba haka ba ne, to mi ya sa aka sami bambanci? Mi aka yi domin a magance matsalolin da aka gani?
- Yanayin aiki : Ko mutane da ma'aikatu (waɗanda abin ya shafa) sun yi abin da ake jira daga gare su? Idan ba haka ba ne, to mi ya sa? Yaya aka tafiyar da aiki, aka kuma sarrafa kuɗi? Wane cigaba aka samu ta fannin ɗorewar aikin?

Ana lura kuma da sakamako da kulawar da aka samu, daga hidimomin da aka aiwatar da su, ta fuskar yawansu da ingancinsu, inda ana bukatar a yi amfani da su domin a cimma sakamakon da ake jira. Ana iya a dubi abubuwa kamar haka: zaman taro na ƙara ma juna ilimi da aka yi, mutanen da aka horas da su, kuɗin da aka kashe wajen yaɗa labarai, saƙonni da abubuwan da aka walalfa, mutanen da abin ya shafa, mutanen da suka yaba da saƙonnin, da hanyoyin da aka isar da su, ds.

- **Auna sakamako da tasiri**

Kowane aiki yana hangen sakamako da tasiri; su ne abin da aka samu ta wurin tafiyar da aiki, da abin da aka samu da ya zama sakewa cikin mutanen da aka nufa, da tsarin da aka yi, da kuma muhalli.

1. **Auna sakamako**

A wannan mataki, ana duban cigaban da aka samu dangance da gurin aikin neman afuwa da aka yi, da sakamakonsa. Wannan ya danganta kenan da gurin da aka ƙayyade ta fuskar sani, da iyawa. Ana iya duba alamu kamar haka: *yawan taruwanni da aka ɗauki nauyinsu, yawan waɗanda suka sa hannu kan neman afuwar, yawan takardu da aka wallafa, yawan wasiƙu da aka rubuta zuwa ga shugabanni, tsawon lokaci da aka ɗauka cikin radiyo/tele.*

2. **Auna tasiri**

Wannan ya shafi sakewa da ta shafi tsari ko yanayin tsarin, ta dalilin sakamako da aka samu ta wurin aikin da aka tafiyar da shi.

## ABUBUWAN DA AKE IYA DUBAWA


AfriMAP, Une evaluation du role de la société civile dans la gouvernance au Mali 2007.

Ashaya, Sam, *Network and Notworking.* Jos: RURCON, 2014

CARE INTERNATIONAL (2001). Advocacy Tools and Guidelines: Promoting Policy Change, A resource Manual for CARE program managers.

CARE INTERNATIONAL (2001). Outils et guide de plaidoyer. Promouvoir le changement des politiques

Graham Gordon : Le guide du plaidoyer, Bien comprendre *un plaidoyer,* Tearfund 2002; www.tilz.info

INTRAC (2008). Advocacy and campaigning. Course Toolkit.

MINALOC (2012). Politique nationale de développement communautaire.

The Futures Group International (1999). Networking for Policy Change. An Advocacy Training Manual. (Sous financement de USAID).

World Alliance for Civic Participation. Civil Society Index 2010, pp.17